A kidime Yafendo ta rarrafo kusada Ya Bala dayai hanxarin toshe hancin sa da hannu 'd'aya, domin warin tusar data saki ba karamin babban bomb bace, Rokansa tashiga yi, kan ya janye ra'ayin sa, ita kuwa Hidaya dake gefe tunani take ina nema Zaria,saurin rufe baki tayi tunanowa da suna tsayawa a garin suyi sallah Idan xasu kano, kuma sun tab'a zuwa dubiyar matar mutumin, sam gidan baiyi mata ba, don mutumin ba mai kudi bane kamar Dr Khaleel (To ai dama hakane, dan mahaifinka mai kudi ne bai xama lallai sai ka auri mai kudi ba, ita dunia ai Up and down ce, kuma dama life is dynamic).

Ya Baka ko takan Yafendo dake bashi hak'uri ya janye 'kudurin sa bai bi ba, sai ma sanya 'kafa dayai ya shure hannun ta, dake makale da 'kafar sa, gyaran murya yayi, kafin yace.

"Saboda haka duk sati mai kamawa za'ai 'daurin auren, Ke kuma Islam sakamakon irin k'ok'arin ki, da yanayin tarbiyarki da kyawawan 'dabi'unki da kike dashi, baki zubarda mutuncin ki ba, ha'ki'ka kin cancanci babbar gudunmawa daga gare mu, amma duk da haka nan bada wani lokaci ba zamu aurar dake, saboda haka da xarar kin samu me son auren ki, ki fada sai ayi bincike ayi auren, sannan yanzu bayan anyi 'daurin auren su Hafsat, zamu nema maki gurbin karatu a jami'a anan garin, zancen fita waje kuyi karatu yanzu an soke shi, Kiyi hak'uri Insha Allahu xamu cika miki burin ki, Medicine xakiyi da yardar Allah, sannan inaso ki je ki nutsu kafin sakamakon ki yafito muji wacce makaranta zaki yi, idanma a Lagos wurina kike so, to duk ba matsala. Allah yasa albarka.."

Haka Inna Bilkisu ma ta sake yin fada mai ratsa jiki sosai, sannan aka watse akabar su Inna suna tsara yadda al'amarin bikin zai kasance.

***

Rana bata 'karya, sai dai uwar 'diya taji kunya, domin ranar asabar da yamma bayan anyi 'daurin auren Nuradden da safe a kaduna, da rana aka 'daura na su Ibrahim, Kabeer, Yusuf. Sai

na ‘Alhaji Saminu Taura da amaryar sa Hafsat Khaleel Mai Mota, sai ‘Alhaji Muzammil Rimi’ da amaryar sa Hidaya Khaleel Mai Mota. A satin ne kuma Nusrah matar Saifullahi ta haihu, tasamu ‘diya mace, aka sanya mata Nabeelah sunan mahaifiyar Saifullahi, amma xa’a dinga kiran ta da Nana.

Yawan mafarkai kala-kala da yawan firgita su Haj Aysa keyi akai-akai , gaba d’aya ta zabge, sihiri ba karya ba kallo d’aya xakai mata kasan jifanta akeyi, hakan yasanya Yakolo yiwa Dr Khaleel shawara kan ya canzawa Aysan gidah. Domin kishiyoyi sun sata a gaba, Hakana Helwa data samu ciki sai ya b’are. Ganin haka yasanya Dr Khaleel gyara wani gidan sa dake kusada gidan su Humairah wato gidan Alhaji Mommodu Mele. Nan ya mayarda Haj Aysa da Helwa, Ai kuwa sun sami sauk’i bayan anyiyyi musu add’uoi sun kuma yi amfani da ganyen magarya. Can gidan kuma yakoma daga Yafendo sai Karimatu, wanda har yanzu ba su sauke ‘damarar shiga malaman da suke yi ba.. Abun dai sai dai muce Allah ya kyauta kawai...

*GIDAN ALHAJI MOMMODU MELE*

Shiirye-shryen tarbar dawowar Khaled ake daga ‘kasar Spain, masu aikine keta kara-kaina........

_WRITTEN BY THE ELOQUENT WRITER:MISS XOXO_🧕🏼
[1/3, 10:53 PM] Miss Xoxo: *_SAIFUL_ISLAM...💕*_

*_NA*_

_*©NANA HAFSAAT*_
*_(MISS XOXO)*_

® *HASKE WRITERS ASSOCIATION*
(_Home of experts and perfects writers)_

*_SADAUKARWA GA:*_

_ASY KHALEEL💕_

*_TUKWICI NE GARE KU:*_
_YA HAJJAH CE😻_
_BILLYN ABDUL😘_

*_SHAFI NA 22-23_*

_SHAFIN YAU NA KUNE ‘YAN GRP DIN *HAJJAH CE NOVELS*, MUSAMMAN *@MAMANSADEEQ💗💗💗 & @PRETTY JIDDAHLURV_ *._INA GODIYA ‘KWARAI DA YADDA KUKE BIBIYAR LITTAFIN *SAIFUL_ISLAM*_

_nanahafsat.wordpress.com_

*GIDAN AJI MOMMODU MELE*

Shirye-shiryen dawowar Khaled akeyi daga ‘kasar Spain, gaba d’aya masu aikin gidan ne keta kara-kaina a kitchen suna had’a masa abinci komai atsare. Lokaci zuwa lokaci Haj Latifa (mahaifiyar sa) kan shiga kitchen ‘din don ganin anyi komai a tsare, kuma cikin tsafta.

Haj Latifa na tsaye jikin kitchen cabinet, tana gyarawa wata mai aiki yadda xata hada ‘coleslaw’. Humaira tashiga cikin kitchen ‘din, tana tafe tana gyara zaman agogon ta dake ‘daure a wutsiyar hannunta. Sanya take cikin abaya baka tayi rolling kanta, hannun ta rike da y’ar purse ‘dinta.

Hannu tasa ta ‘dan gutsiri maras da ake yayyan kashi ta jefa a bakin ta, kafin tace,

“Umma. Zanje gidan su Islam, zandawo kafin a ‘dakko Ya Khaled a airport.”

Kad’a kai Haj Latifan tayi, kafin tace,

“Karki jima Humaira, nasan halin ku idan kuka had’u da Islam.”

“Insha Allah Umma.. Sai na dawo” ta fada tana ficewa daga kitchen din

“Allah ya tsare... “

Sai kuma ta juya wajen Kande mai aiki, tana gyara mata yadda take ‘kokarin danna naman akan abun gashi.

“Ha’a Kande ki bari naman yayi marinating kafin kiyi grilling mana haba.”

*DR KHALEEL’s*

A kitchen Humaira ta tarar da Islam tana tuk’in tuwo, ta rage gas tana jiran ya turara ta sauke shi, da gudu Islam tai hugging Humaira cike da jin dad’i, Humaira ta yatsine fuska tana bin Islam da kallo,

“Ke kam kinason girki, ‘karama dake kike girki? bayan ga masu aiki.”

Girgiza kai Islam tayi, tana jaddadawa Hari mai aiki ta kwashe tuwon, cikin murmushi tace da Humaira,

“Babes, wallahi tun banaso sai da na koya, Ammi tace hakan nada kyau idan nayi aure na huta, Ai kuwa tuni yanzu kinga yadda na iya abinci kala-kala kuwa?”

Tabe baki Humaira tayi, kafin tace.

“Hu’uhm! Ni kuwa na tsani girki, kuma idan nayi aure masu aiki Umma xata dakko su dinga yi mun”

Kad’a kai kawai Islam tayi, taja hannun ta sukai sama, dakinta suka shiga, Animation cartoon ta saka musu na ‘princess and the frog’. Suna cikin kalla Lee tazo, nan suka kafa dabar hirar school, zancen auren su Hidaya ya shigo, Humaira ta tsunture da daria tana rufe baki, kafin tace.

“Naga mazajen su Hafsat a album na ‘daurin aure, wannan ai sun haife su.”

Lee ce ta amshe tana,
“Maganin su kenan, sun janyo at early age anyi musu aure.”

Islam dake gefe ta katse su tana daga hannuwa,

“Abeg abeg, enough. Su ai yanzu sun huta tunda sunyi auren su.”

Lee da Humaira suka tafa, suna kyalkyala daria, kafin Lee tace.

“Kowa zeyi ai, ni kin tunomin ma Dawood ya isheni da maganar aure wallahi, nace mishi ni ba yanzu xanyi aure ba yaki yadda”

Humaira ta kwashe da daria,
“Wallahi nima Yaseer ya isheni, nace mi shi sai na zama accountant tukun sa..”

Lokacin jin Islam ya dauke, tuni ta fada duniyar tunani. Ita kam haka xata xauna ba xatai aure ba kenan? Shin me tayiwa maza da ba sa sonta haka?, Ta jima tana tunani sai da zazzafan dundun da Lee ta zuba mata a baya ya dawo da ita dunia. Cikin daria Lee tace,

"Haba girly, tun daxu muke magana kinyi shunning dnmu, bama wannan ba tashi mu raka Humaira gidah, brother dinta ya dawo."

Mikewa Islam tayi, a tare suka sauka kasa parlorn Hajia aysha suka mata sallama, sannan suka tafi gidan su Humaira.

*GIDAN ALHAJI SAMINU TAURA*

Zaune Hafsat take tana tsiyayar da hawaye agefen murhu, tunda aka kawo ta gidan take aikatuwa, Haj Larai babbar matar Alh Saminu ta takura mata da tsangwama, yau ma dakyar ta iya 'karasa tuka tuwo a babbar tukunya mai cin kwano biyar, duk ya 'kone ya koma tamkar amala.

Daga 'dakin ta Haj Larai tafito, da yake kowannen su 'daki d'aya da parlor ne mallakin sa, sai yammata xagada xagada 'yayan Haj Laran, wanda kowannen su ya girmewa Hafsat nesa ba kusa ba. Rissinawa Hafsat tayi tana cewa,

"Aunty na kammala.."

Ashar Haj Larai ta lailayo ta 'durawa Hafsat, Tare da bata kyakkyawan ranqwashi a 'kwanyar kanta,

"Yanzu ke a gidan uban ki haka ake tuwo? Okay na tuna fa ke shafaffiya ce da mai, renon kwanfilas (cornflakes), to bari kiji bar ganin Alhaji na rawar takashi akan ki, wallahi tallahi idan kika ci gaba da 'kona abincin gidan nan sai na lahira ya fiki jin dad'i."

Cikin tsawa ta sake cewa,

"Wuce ki bani waje, banza mamugunciya, jia kin dafa taliya ta koma tamkar kunu, yau kin maida tuwo kamar.."kasa 'karasawa tayi tana haki, cikin iko tasa babban hannun ta tana dungure mata kai.

Bata hak'uri tayi had'e da yin sum-sum ta mike ta koma 'dakin ta, lokaci xuwa lokaci hawaye ke y'ar tsere akan fuskarta, a hankali cike da tausayi take mai-maita,

"Innalillahi wa'inna ilaihir raji'un"

*GIDAN ALHAJI MUZAMMIL RIMI*

Hidaya ce tsaye a tsakar gida tana tular wankin braziers da su pants na ‘yammatan Haj Deluwa matar Alhaji Muzammil, tana yi tana d’aga hannayenta tana share gumin dake kwararo mata,

“Ke..” Fareedah babbar ‘yar Haj Deluwa takira Hidaya,

“Na’am” Hidaya ta amsa jikin ta na ‘bari.

“Ungo nan ban had’a miki da shi ba, yanzu na cire shi, kisa hypo ya wanku tatas..”

Sa hannu Hidaya tayi ta karba tana kukan zuci. Domin pant ne gaba d’aya ya jike da jinin al’ada, sai ‘karni yake.

A ruwa ta jikashi tana mai canza mai ruwa lokaci zuwa lokaci. Sosai tafara hawaye ganin Fareedah tabar wajen. Ko’a mafarki bata tab’a tsammanin irin wannan rayuwar ba, ita kanta panties dinta a washing machine take sa su lokacin da take Abuja, amma yau wai itace mai wanke na wasu mai ‘dauke da jini, jinin ma na al’ada. Wani abun takaicin ma Haj Deluwa idan ‘yan rashin kirkin suka tashi har sakar ‘duwawu takeyi ta narka uban kashi ta kuma tashi ta barshi, Hidayan kuma ya xama dole ta kora ruwan(flushing). Da dare kuma Alh Muzammil ya maida ita sex machine, budurinsa yake akanta, ko tunanin ita ‘din yarinya ce baya yi.

*BAYAN WANI LOKACI*

Sosai Islam shakuwa ta shiga tsakanin su da Khaled , takanas yake zuwa har gidan su suyi hira, ko kuwa ya kira ta wayar Ammin su yaita janta da hira, hakan ya sanya Islam sawa a ranta lalle khaled sonta yake da aure kuma.

Ganin irin muguwar shakuwar da sukai, Humairah ta tseguntawa Umman su wai soyayya Islam da Ya Khaled suke yi, cike da jin dad’i Haj Latifa ta samu Khaled da maganar Islam, tashin farko ya kwaso rantsuwa ya dire tare da ‘doriyar,

“Tab! Umma kenan. Ni wallahi ba son Islam nake da aure ba, na ‘dauketa tamkar Humaira a zuciata, kuma yarinyar she’s fun to be with. Tanada ‘ko’kari..”

“Naji-Naji... Amma duk wannan alamun soyayya ne Khaled, wallahi yarinyar mutuniyar ‘kwarai ce, kuma mahaifiyar ta baka ga yadda muke mutunci ba..”

Daria Khaled ya shiga yi harda rike ciki, harara Haj Latifa ta xabga masa ,hakan yasanya shi rage sautin dariar sa, cikin gaskiyar sa yace.

“Allah Ummah.. Dagaske ba son Islam nake ba, already ina da wadda nake so wallahi, kuma har munyi alqawarin aure”

Fushi Haj Latifa tayi da Khaled, ta mike tai ficewar ta, shi daria ma abun ya bashi wai suna soyayya da Islam, yana cikin daria wayarsa tafara ‘kara, Islam shine sunan dake yawo akan screen din wayar sa, ‘dagawa yayi ya kara a kunnensa,

“Hello Ya Khaled” zazzak’ar muryar Islam ta doki kunnen shi.

“Sisto!” Yafada yana ‘kara gyara kwanciyar da yai akan pillow.

“Ya Khaled inason maka wata magana.”

Mikewa yayi yana gyara button din rigar sa,

“Magana sis? Yaushe kikeson gani na?”

“Ko yanzu ma.” Tafada tana jan ‘maa din.

“Okay I’m on my way.”

Ya katse kiran bayan sunyi sallama, a gaggauce ya canxa kayan jikinsa ya fesa turaruka, da kafa ya tafi gidan su Islam domin ba wani nisa. Yana zuwa ya kirata. A parlorn baki ta same shi, sanye take cikin laffaya baka tayi kyau sosai. Cikin salon maganar sa dake tafiya da ‘yammata yace,

“Kinyi kyau Mi lady.”

Murmushi tayi tana wasa da zoben yatsanta. Cikin shagwababbiyar muryar ta tace,

“Ya Khaled ina yini?”

“Lapia lou kanuri babe.. Ya su Ammi?”

“Ammi tana parlor, lalle ake mata”

Kad’a kai yayi yana sipping ruwan data kawo masa, yasha sosai kafin yace.

“Toh Mi Lady gani ko”

In’ina (stammering) tashiga yi,

“Ya Khaled da..Dama.. ca..nai”

“Menene Mi Lady uhm?” Yafada yana sake komawa kujerar dake kusa da tata.

Rufe fuska tayi, kafin cike da kunya tace.

“Ya Khaled, dan Allah kazo muyi aure, tunda kaga muna soyayya da kai.”

Baki bude yake kallon Islam, inde shirin da suke ta dauka soyayya ne, lalle ya yadda batasan meye soyayya ba, ba kuma tafara taba har yanzu. Cikin dakewa yace,

“Ni zaki aura? You are not serious” Yafada hade da mikewa tsaye.

Durkusawa tayi tana k’ok’arin zubar da hawaye,

“Wallahi Allah ina sonka Ya Khaled, dan Allah ka yadda ka aure ni kar ayimin auren dole, Na yadda ko ranar daurin auren ne kace kafasa aure na dan Allah, ko kuma ka...”

Dakatar da ita yai, ta hanyar ‘daga mata hannu, cikin ‘dagawar murya yace,

“Haba Islam, dududu shekarunki nawa? Idan kinyi nisa kiyi sha takwas, shirin da muke irin na yaya da ‘kanwar sa shi kika ‘dauka a matsayin na saurayi da budurwa? kowa da kike gani idan har Allah yayi yanada rabon aure wallahi zeyi, kuma wani baya auren matar wani, haka zalika wata bata auren mijin wata. Duk inda kike a fadin dunia wallahi mijin ki na nan zuwa, Kiyi hak’uri Islam, wallahi ni ba son aure nake miki ba, na daukeki a zuciata tamkar Humaira. Kisani cewar slowly but surely khairan Insha Allah... Naki readymade din mijin na nan zuwa, wanda yafini komai da izinin Allah. Kiyi hak’uri pls , ki yafemin dan wallahi inada wanda naiwa alqawarin aure.”

Yana gama fada ya fice yana goge hawayen dake neman zubo masa, Islam kuwa tuni ta sulale awajen tana kuka mai tsuma zuciyar duk wanda ya saurara, a yau takara tabbatarwa ita din bakin jini ne da ita, wanda lokaci d’aya ta cire soyayya da son aure a ranta. Dakyar ta iya mikewa ta koma sama, Ya Bala takira a waya ta sanar masa da tananan zuwa wani satin Lagos, zatai hutu kafin su fara lectures a nan Nile university dake Abuja.

***

Khaled yana komawa gidah ya hada kayan sa a akwati, sallama yaiwa Umman su kan zaije Lagos gidan Uncle Faruk( wan babansu) ya ‘dan kwana biyu kafin Vissa d’insa tafito ya koma Spain ‘karo karatun Masters.

Bata hana shi ba, domin fushi take dashi, ita ta dauka akan maganar da sukai da ita ne daxu yasan yashi ‘kaura daga garin, Batasan yayi hakanne don ya baiwa Islam lokaci ta cire sonsa a ranta.

*LAGOS*

Karfe 5 dai-dai jirgin su ya sauka a airport din Murtala Muhammad dake Lagos. Dakyar Khaled ya ciro waya ya kira Uncle Faruk cewar ya iso azo a ‘dauke shi.

Dake weekend ce Alhaji Faruk Muhammad(Uncle Faruk) yana gida da iyalin sa, matar sa Haj Zuwaira ita kadai ce sai ‘ya’yan sa mata biyu, da maza biyu.

Aisha, Fatima, Adnan sai ‘dan autan su dake karatu a America mai suna... *SAIFULLAH*

_WRITTEN BY THE ELOQUENT WRITER; MISS XOXO🧕🏼_
[1/3, 10:53 PM] Miss Xoxo: *_SAIFUL_ISLAM...💕*_

*_NA*_

_*©NANA HAFSAAT*_
*_(MISS XOXO)*_

® *HASKE WRITERS ASSOCIATION*
(_Home of experts and perfects writers)_

*_SADAUKARWA GA:*_
_ASY KHALEEL💕_

*_TUKWICI NE GARE KU:*_
_YA HAJJAH CE😻_
_BILLYN ABDUL😘_

*_SHAFI NA 24-25_*

_SHAFIN YAU NA KI NE *ZEE YABOUR* xeexeecism 😘Habeebtyn-Habeetyn baby Yasmeen💕Allah ya ‘kara basira ki cigaba da wantsalo mana FETTA_

_nanahafsat.wordpress.com_

Alhaji Faruk Muhammad ‘dan uwan Alhaji Mommodu Idris ne.Yaya ne ga Alhaji Mommodu domin iyayen su daga tsatso ‘d’aya suka fito. Ma’ana ‘dan wa da ‘dan ‘kani suke. Mahaifin Alhaji Muhammad Idris shine Yayan mahaifin Alhaji Faruk Muhammad. Zaman sa ya koma hannun mahaifin Alhaji Muhammad, domin iyayen sa duk rasuwa sukai. Anan yai karatu, har Allah ya kai shi babban matsayin da yake na likita, (surgeon).

Ya hadu da Mahaifiyar su Saifullah, wato Hajia Zuwaira a garin kano,’ bangaren galadanchi, a asibitin Aminu kano. Lokacin ita kuma sun kawo mahaifin su baida lapia, anan ‘kauna ta’dore mai tsanani har ta kai ga aure.

*4:00pm*
LAGOS (IDIROKO, MARYLAND)

Zaune Islam take, hannunta rik’e da Novel ‘din, ‘chasing Red by Isabelle Ronin’. Kusan kullum hakan take ko dai kaga Qur’an, ko littafin daya ‘kunshi harkan medicine, sai kuma novels, da suka zamar mata addiction.

Farida (Riri) ‘kanwar Haj Nabeelah ce, a gidan take a zaune tun lokacin tana ‘karama, domin sa’ar su Islam ce, tashiga ‘dakin da Islam take, zama tai akan gadon tana duban Islam da sam batasan shigowar tata ba,

“Peek a boo” Riri tafada da ‘karfi tanawa Islam gwalo, Ai kuwa Islam din ta ‘dan tsoro ta, harararta tai cikin wasa tana tura baki gaba,

“Toh shagwab’abbiya, ke kam mijin ki yaga ta kansa da tsagwaran autanci, to ni dai tashi maza, zamu ‘danje outing kiga gari.”

‘Dan yatsina fuska Islam tayi, kafin tace.

“No, not today pls, banason katse karatu na”

“Ke wallahi baki isa ba, Haba yarinya sai kace kunkuma, sannu matar ustax. Kullum kina ‘daka kamar sabuwar amarya, da anyi magana kice this and that, abeg tashi muje nan kusa ne ba jimawa zamuyi ba.”

Takaici kamar ta shak’e Riri haka take ji, a dole ta shiga band’aki ta ‘karayo wanka. Doguwar

riga ta saka mai launin sararin samaniya, ta yane kanta da mayafin rigar. Fita sukai itada Riri', domin su kad'aine 'yammata a gidan yanzu, duk kowa ya watse. Mazanma sai dai 'yan uwa na 'y'ar gaya ko 'yan uwan matan Ya Bala 'din.

Riri ce ke driving, wani joint suka je, ba abunda akeyi sai zuk'ar shisa, joint ne daya amsa sunan joint, domin clubbing ne na maza da mata, sai raye-raye akeyi ana busar shisa. Gefe d'aya kuma kayan 'kwalam da ma'kulashe ne. Gaba d'aya Islam kallo d'aya xakai mata kasan a matukar tsoroce take, domin sai takurewa gefe d'aya take a bayan Riri, musamman da idanun maxan wajen ke kanta. Wani table mai cin mutum biyar suka xauna, bayan Riri ta babbasu hannu sun gaysa gaba d'aya maxan wajen da matan had'e da kyakkyawar runguma da sumba a gefan kumatu.

Kan kace me? Table ya cika da maza, harda wanda suka jajjanyo sit dinsu dawo kusada Islam, ita dai sai raba ido take tana binsu da kallo, domin san bata taba engaging kanta a irin wannan abubuwan ba, addu'oi kawai take a zuciyar ta, na Allah ya fiddasu lapia daga wannan wajen, had'e da cin alwashin sai tayiwa Riri tatas, data kawo nan wajen.

Leefa d'aya daga cikin mazan dake table din ya kai hannun sa zai taba cinyar Islam, da sauri Islam ta matsa tana bige masa hannu, ware ido yayi yana duban Riri alamun tambaya, daria Riri tayi tana kashe masa ido d'aya kafin tace,

"Uhm uhm Leefah, Bar wannan scaredy-cat ce, ko mọ ohunkohun" (batasan komai. Ta fad'a cikin harshen Yoruba.)

Kamar maye haka Leefa ya tsaya yana duban Islam, kakkauran miyau ya had'iye, tamkar yaga wani nama. Kafin cikin harshen yarabanci yace,

"Mo rii o, chai ọmọbirin naa ni ara."
(Nagani, Kai amma yarinyar nada jiki mekyau).

Ita dai Islam batasan mai suke fad'a ba domin ba jin yarabanci take ba, haka ta xauna kamar kurma, duk wanda yazo wajen haka yake 'karar surutunsa ya tashi ya tafi, kanzil bata had'ashi da Islam. Ji take kaman ta tashi tabar gurin, matsalar batasan kan garin bane, da tuni ta ware gidah.

Tana ganin yadda maza suka saka Riri a tsakiya suna shafata, su kisses and hugs, touch-touch duk shi sukeyi, sam bata lura ashe shegun kayane ajikin Riri ba sai yanzu, domin wata figaggiyar vest ce da wando leggings, sai ta 'dora jilbab har 'kasa akai. Yanzu kuwa da sharholiyar tasu tayi yawa, tuni Leefa ya fige shi gaba d'aya yana yadda yaga dama da jikin Ririn.

Baki, hanci kai harda idanuwa Islam ta gwalalo tana duban su Riri, dakyar da kamo addu'oi ta janye kallon ta daga garesu, tana neman gafarar ubangiji daya yafe mata wannan zinar ido data

gani.

Sai gab da magrib suka koma gidah, Sam Islam bata bari sun hada ido a mota da Riri ba, hakama ko magana Ririn ta ‘dakko, ita dai Islam nata uhm da uhm uhm ne kawai, har suka ‘karasa gidah.

Sai bayan sunyi shirin kwanciya ne Islam ta d’akko zancen da,

“Riri meyasa kike aikata abunda kinsan haramunne?”

Yatsina fuska Riri tayi, domin tasan za’azo wajen, ganin yadda Islam din tayi sak ‘daxun, tasan sarai tanada tarin tambayoyi akanta,

“Anzo dai-dai wajen kenan, Toh malama menayi wanda Allah ya hana?”

Tasowa Islam tayi ta kama hannun Riri cikin nata, kafin tace,

“Riri, yadda naga kuna tab’e-tab’en junan ku sam ba a jiyan kuka fara ba, da alamun kin dad’e kina zuwa wajen.”

Dogon tsaki Riri taja, kafin tafara ‘babbaka daria,

“Kina nufin ki cemin bakya rage zafi ke? Kenan ke ko ‘dan kiss baki taba yi da wani ba, wai ke a hakan kina nufin kice ko gaisawa da maxa bakyayi?! Talk less of se....”

Katseta Islam tayi tana girgixa mata kai,

“Wallahi tallahi bantab’a ba, ni dai da hankali na, na tab’a namiji ko na rungumeshi kai har kiss yashiga ko gaba da haka ma, wallahi ban tab’a ba, Nasan nayi mix school amma irin haka be tab’a faruwa da ni ba. Allah shine shahidi.”

Gyada kai Riri tayi, kafin cikin tabe baki tace,

“Ke yanzun wallahi rayuwar sai da dan tab’e tab’en kake aure, kashi sittin na ‘yammata abunda sukeyi kenan, kuma su ne ke auruwa, amma xakiga yarinya kullum cikin hijabi ko babban mayafi wai ita saliha, to wallahi maxan yanxu basason wa’ennan, domin gani suke ai basu waye ba.”

Tunani Islam tashiga, ganin kuma wallahi hakanne, tasan wanda suke hakan kuma suke auren, babban misali gashi nan yafaru dasu Hafsat, ita dake lullube jikinta tana hana maxa tab’ata ai gashi batai auren ba, ko saurayi batada shi ma, duk gudunta suke, kamar wata mujiya mai ba’kin jini.

Ajiyar zuciya ta sauke kafin tace,

"Hakane Riri, gaskia yanzu slay queens ke aure, amma idan kika auna abun a mizanin hankali, zaki ga cewar ai Allah yayi hani mace da namiji su keb'e ma, talk less tab'e tab'en juna.

"Toh madalla shekiya malama ustaxiya Islam, rike shawararki banaso, ki nanan Kina killace jikin ki tayaya xasu gani suce suna sonki? Ni kuwa wallahi sai hamdala samari harda na siyarwa sai na sayar."

Murmushi kawai Islam tayi, kafin ta mike tashiga band'aki.

*ABUJA*

Zaune Haj Karimatu da Yafendo suke, sai 'kus 'kus sukeyi, bakajin 'karar komai sai 'karar TV, Karimatu dake aikin taunar chingum taja wata shegiyar majina kafin tace,

"Ai wallahi tallahi tunda y'ar iskar matar nan ta shiga tafita don ganin anyiwa 'yayanmu fyade, bata hakura ba ta sake bunka tsafin nata, tasa santolon (Dr Khaleel) yai musu auren dole, to wallahi baxan yadda ba nima, sai nayi mai yiwuwa rayuwar tata 'yar ta lalace, ta 'kas'kance, ta shiga dunia, sai ta maida gidan can bariki, taxama gansamemiyar karuwa."

Tana fad'a Yafendo na jinjina mata hannu, kafin tace.

"Wallahi kuwa Yaya, ai bazamu yadda taci banza ta kwana lapia ba, yo bana gaya miki danaje wurin na 'kan tudu' mai yace ba? 'Kwarya ya nuna min yace ki kalla na minti 5, duk fuskar da kikaga ta fito, to itace mai yi muku sihiri, duk wani cigaban ku ta datse shi, kamar wajen tafiyar ruwa agine shi. Abunda yace kenan, yace kuma wallahi dana kawo wannan million biyar 'din, da saniyoyi uku, da tattabaru biyu farare 'aure', da sabon haihuwa 'kyan'kyashasshen 'kadangare, yace kamar 'kiftawa da bismilla, rayuwar Aysa xata tagayyara. Za'ai mata kurciya tabar garin anemeta arasa, xa'a sanya mata hauka, sannan duk 'ya'yanta na gidan aure zasu rabu da mazajen kowacce ta shiga dunia ta lalace, ita kuwa Islam nace yayi me yiwuwa ai mata fyade mai cike da 'kas'kanci, a tura mata ba'kaken aljanu su hanata aure, nace ya 'kara mata da tsumammen d'oyi, ta dinga hamami duk inda taje mutane su dinga gudunta kada su rab'eta..."

Daria Karimatu ta shiga bankawa, Yafendo na taya ta, sai da sukai mai isar su, kafin Karimatu tace.

"Ai Insha Allahu zuri'ar Aysa kaf sai sun tagayyara, sun shiga 'kuncin rayuwa mai cikeda tausayawa..."

Sam basusan duk maganar da suke an d'auke wuta ba, Dr Khaleel dake tsaye yagama jin duk zantukan da sukai, hawaye ne ke gangarowa daga idanun sa, dakyar ya iya sanya kansa ya

shiga parlorn bakinsa d'auke da sallama..

Dede lokacin, Yafendo da Karimatu sun had'a baki wajen fad'ar,

"A hayye nanaye..."
'Casss' suka had'a hannuwa, suna tafawa.

Ganin sa yasa duk suka shiga nutsojin, Karimatu cikin ki'dimewa tace,

"Yawwa Yafendo sai ki fara wanke alba...."

Bata k'arasa ba Dr Khaleel ya 'daga mata hannu, alamar ta dakata...........

*USA 🇺🇸*
Harvard University (Cambridge)

Saifullah ne zaune a garden na school hannun sa rik'e da wata paper yana zana(drawing) wani gini dake can gefan inda suke a zaune, lokaci zuwa lokaci yake dan 'daga kansa yana gyara zanen,

Zaune suke da sam, Jeremy sai Abbas (Abbas abokin sa tun na farkon littafin da su kaje Lagos tare), kowanne da abunda yakeyi acikin su, cikin haka wata matashiya 'yar Nigeria ce itama, da kallo d'aya xakai mata kasan Hausa-Fulani ce, mai suna Ameerah wadda ake kira da 'Meerah'.

Zama tai a kujerar da saifullah yake, ganin ta yasa ya saki tsaki a hankali, tamkar yaga kashi, ya mike yana karkade jikin sa, ya koma d'aya kujerar, bata damu ba, ta fadada murmushin ta, siraran hakoranta suka bayyana, kafin tace,

"Genius" (haka suke kiran saifullah a school din, saboda k'ok'arin sa).

Tamkar bai jita ba, ya cigaba da abunda yakeyi, sau uku tana kiran sunan sa, mikewa yayi xai bar wajen Abbas yai hanxarin riko hannunsa yana girgixa mai kai, alamar a'a. Cikin rad'a yace mai,

"Ka saurareta pls, stop shunning her, Kaga masu jajayen kunnuwan nan sai suyi mana daria."

Cewar Abbas, yana fada kuwa ya kira su Jeremy kan su koma su zana wani sabon waje a bayan school din. Suna barin wajen ta 'dan durk'usa tana niyyar kamo hannunsa, saurin janyewa yayi yana galla mata harara, da manyan idanunsa TubarkAllah. Cikin daddad'ar muryar sa, so melodious and sweet yace mata,

"Pls respect your self Ameerah... Respect is reciprocal, ke macace, maintain your dignity and

decency, ta haka xakiyi earning respect. And secondly, na fada miki several times cewar ki abiding rules d'ina. My time is priceless, inada lokacin komai pls, yanzu ina cikin aiki kin katseni, bayan na miki warning yafi a 'kirga.."

Ita sam ba maganar da yake ce ta dame ta ba, sanyayyar muryar sa me kama da sarewa itace ke tafiya da ita, har wani lumshe idanu take. Tsaki Saifullah ya saki a karo na ba'adadi. 'Dan buga drawing pen d'insa yayi akan seat din da take, juyawa tai tana binsa da kallon soyayya.

"Ameerah.."

"Na'am"

tafada cikin za'kuwa, don ba karamin dadi take jin yadda yake kiran sunan taba, aganinta yafi kowa iya fada ma.

"Get lost pls..."

Ajiyar zucia ta sauke, kafin ta tashi dakyar ta tafi, tana tafiya tana kallon sa, gaba d'aya she's half naked, kayan da tasa sosai suna nuna surar jikin ta, cikin fusgar da iskar bakin sa, ya furta..

"Sam ba kamin kai.. ughh! so annoying"

****

_Assalamu Alaykum sisters_

_Masu maganar ban kyauta ba dana had'a saifullahi da Nusrah, akan lallai mai yasa ban kashe Nusrah na aura mai Islam ba? kuyi hak'uri sannan ku fuskanci wani abu d'aya🤗 Na taba rubuta saifullahi yana son Islam?! No bantaba ba, Tabbas nace sha'awarta yake ba sonta yake ba, haka zalika bance Islam na son Saifullahi ba, sai dai ko Khaled. Ko a gaske sha'awa ba soyayya ba, bata da dad'i. Domin da mutum ya kauda wannan sha'awar tasa, to fa daukar macen xaiyi kaman fankon ashana, batada wani amfani, sai dai idan Allah ne yayi dama dole sai ya xauna da 'ita har 'k'arshen rayuwarsa, Abu na biyu wallahi dama haka na tsara littafi na da sunan su su biyu, *SAIFULLAHI* cousin din Islam, sai kuma *SAIFULLAH* wanda zai zama mijinta nan gaba, Saboda haka ni bana tab'a canxa yanayin yadda na 'dakko littafi na, yadda na tsara haka nake tafiyar dashi, bana canza aqalar alqalamina, yadda sauran littafai suke nawa yasha banban 🤗Abu na biyu kowa da irin farin jinin sa pls, yakamata adinga saka reality into fictional stories, shi farin jini kowa da yanda Allah yayi sa, wata na dashi sosai kuma lokaci d'aya take aure, Saboda yawan masu sonta, wata nata ga maxa rututu amma bana auren, wata kuwa babun badhiluhu ne😉ma'ana duka babu digon farin jinin balle samari. So yakamata ku 'dauki hakan a sabon salo🙏🏾dole ne kowane littafi sai yarinya tayi farin jini?😫 duk inda tai farrr samari kamar ruwan sama😒 ku barni na 'karasa littafi na pls kamar yadda na tsara shi, ta yadda xamu gane akan me ya fadakar😻idan ba haka ba😕Toh zanyi shafi d'aya na gama shi a haka, duk mutaru mu kasa fahimtar akan me aka yi shi🤣😉_

_Conclusively Hafsatu fa na da ciwon idanu. Thou nasan yawanci kun sani, Yes da glass nake amfani sometimes🤗. _ _so I can't be squeezing and pressing my precious eyes anyhow ba😹 kunsan ido sai ana d'an lallab'ashi, _so typing da nake yawan yi babu break, yasanya idanun fara fushi yana hautsinewa😌xamu fara 'diban break.._
_With love,_
_ME, MY EYES AND MY GLASSES 😹🙏🏾_

_WRITTEN BY THE ELOQUENT WRITER:MISS XOXO🧕🏽_
[1/3, 10:53 PM] Miss Xoxo: *_SAIFUL_ISLAM...💕*_

*_NA*_

_*©NANA HAFSAAT*_
*_(MISS XOXO)*_

® *HASKE WRITERS ASSOCIATION*
(_Home of experts and perfects writers)_

*_SADAUKARWA GA:*_
_ASY KHALEEL💕_

*_TUKWICI NE GARE KU:*_
_YA HAJJAH CE😻_
_BILLYN ABDUL😘_

*_SHAFI NA 28-29_*

_INA 'YAN GROUP 'DINA NA, *HOME OF NOVELS*?, TO KU MATSO KUSA, SHAFIN YAU NAKU NE SISTERS😘KUYI YADDA KUKA GA DAMA DASHI, JAZAKUM ALLAH KHAIRAN! DA YADDA KU KE BIBIYAR LITTAFIN, *SAIFUL_ISLAM💕* _

nanahafsat.wordpress.com

Gyaren murya Ya Bala yayi, yana mai nuni da su Haj Karimatu. Da yatsan sa na biyu dake hannun daman sa, cikin muryar fushi dake tattare da damuwa yace,

"Hakika kun bani mamaki, yadda na 'dauke ku, ashe kun xarta hakan, wannan wacce irin musibace? Shin kuna tunanin duk abunda kuke yi Allah baxai kama ku da laifi ba ne ko kuwa? Wane irin haukan kishi ku ke yi ne ? Da ya xarta tunani? Ni da ku, shekarun baya na ja muku kunne, had'e da tausasa zuciyar Khaleel, ya hakura ya dawo da ku 'dakunan ku, dukkoda yadda kuka 'kulla sharri akan yarinyar da batada masaniya akan hakan, daga ni sai ku, sai su Khaleel, aka rufe maganar ba'a bari tafi to ba. Sai daga baya na gane ba kishi bane, tsantsar mugun tace.. Tirr! Da hali irin naku wallahi."

Shiru yayi, gaba d'aya ya rasa mai zai sake cewa, ganin haka, yasanya Inna Bilkisu dake gefe cewa,

"Duk dan akan kishi kuke hakan ko? Shinma menene kishi? Tunda naga kamar bakusan ma'anar sa ba, da yadda ake yinsa. Shi kishi wani yanayi ne na so  da kauna da burin kare abun da ake son daga kamuwa da cuta. Ana kishin kasa kuma ana kishin sana'a da abokan zama.. Duk inda akwai kishi mutane na ganin cewa akwai so, har ma wasu kan ce "kishi so ne". Duk dan Adam bai cika mutum ba sai ya kasance yana da kishi. Ko dai ya kasance yana kishin kansa, kishin iyalinsa da dai makamantansu.,

"Hausawa na cewa "kishi kumallon mata." Amma a zahiri ba mata kadai ke da kishi ba, har mazan ma suna da shi. Mutane da dama na ganin cewa maza sun fi mata kishi, kawai dai matan sun fi nunawa ne. Wannan abu ne da za a iya muhawara a kai. In har hakan ne, akwai abubuwa da dama da ke silar hakan. A addinin musulunci da kuma al'adar mutanen Afirka da yankuna da dama, maza ne suke auren mace fiye da daya. Su kuma mata miji daya kadai suke aure. Wannan shi ke sa mata su yi ta jin tsoron kawo musu abokiyar zama wadda ake kira kishiya. Kalmar kishiya kanta bai dace ana fadar ta ba, kasancewa zama aka zo yi tare da miji daya ba wai wasa ba. Ita kalmar ke kara wa mata da dama tsoro cikin zukatansu da zarar an furta ta. Sannan kuma maza da dama sukan fara wulakanta uwargida idan amarya ta zo. Ita da 'ya 'yanta su zama ko oho. Su ma amaren su yi ta jin dadi cewa ana wulakanta uwargida, ba sa tunanin cewa su ma idan aka yi sabuwa, haka za a yi masu. Hakan na matukar tsoratar da mafi yawancin mata, har ma ka ji suna cewa "ba kishiyar ake tsoro ba sai sharrin ta,

"Yarda da amincewa na da matukar muhimmanci a dukkan tarayya, musamman ma ta aure. Da zarar babu yarda a cikin zaman aure, zargi zai shigo ciki kuma ba za a taba samun zaman lafiya ba. Ya kamata mu rika gina aure bisa yarda da amincewar juna, don hakika su ne gishirin zaman aure. Rashin yarda ne ke kawo rashin jituwa har ta kai ga rikici, a wasu lokutan ma har da kisa,

"Kusani cewa, Kishi wata dabi'a ce da Allah ya halicci mata akanta, Nana A'isha tana cewa : "Ban taba yin wani kishi ba, irin kishin da na yiwa Khadijah, duk da cewa ban taba ganinta ba, saboda yadda na ji Annabi s.a.w yana ambatonta" Bukhari 1388, Kishi mai tsafta, shi ne :

kishiya ta yi rige-rige da kishiyarta, wajan kyautatawa mijinsu, Akwai Jahilci : ta yadda mata da yawa suka jahilci, hikimomin da suka sa Allah ya yi umarni a kara aure, kamar;rage yawan zawarawa da 'yammata, da kuma yawaita zurriyar Annabi S.A.W.,domin da za su kalli wannan da kishinsu ya ragu. Mummunan zato, yawanci uwar gida tana tarbar amarya da mummunan zaton cewa za ta rainata, haka ita ma amarya ta kan zo da mummunan zaton cewa ba za su yi zaman lafiya ba da uwar gida, wannan sai ya sa daga zarar sun hadu babu wuya sun yi rigima.Amma idan da ace kowacce za ta tarbi kowacce da kyakykyawan zato, har ta ga kamun ludayinta da ba'a samu matsala ba.,

"Rashin adalci daga wajen namiji, yawanci maza su kan karkata zuwa amarya, wannan sai ya haddasa fitina, saboda uwar gida za ta ta ce ba ta yarda ba. Amma idan kuka duba anan zaku ga cewa, shi maigidan ku sam ba haka yake ba, hakika yana k'ok'arin adalci a tsakanin ku, Saidai abin da ya kamata mata su fahimta shi ne : babu yadda za'a yi namiji ya hada mata biyu face sai ya fi son daya, Annabi s.a.w. ya zauna da mata tara kuma ya fi son Nana A'isha, har ma mutane sun fahimci haka, wannan ya sa idan za su yi masa kyauta, sukan 'kirkidi ranakun da yake dakinta, don sun san kyautarsu za ta fi karbuwa a ranar, don haka idan kika ga mijinki ya fi son kishiyarki, ki yi masa uzuri kar ki tada fitina, saidai abin da sharia ta hana shi ne, rashin adalcin ya fito a hidimomin yau da kullum. Wanda ku Kan ku kunsan maigidan ku na kamanta adalci a tsakanin ku, sannan akwai Munafukai, masu cece-kuce, idan da ace kishiyoyi za su daina daukar guzuri-zoma, ta yadda idan suka ji magana za su tabbatar da ita kafin su yi hakunci ga kishiyarsu da hakan ya rage kawo matsaloli. Amma ku duk kunyi fatali da wannan idanuwan ku sun rufe, kun 'dauki zugar shed'an kun d'orawa zuciyar ku, kuna aikata shirka, domin wallahi had'a Allah da wanin sa shirka ne, zuwa wajen duba, da yan tsibbu suna gaya muku 'karya da gaskia, kuna zama akai, kun cusa mummunar 'dabi'a aranku, kun 'dau wani qudri na ganin kunyi mai yiwuwa kun fidda wasun ku daga gidan, to ku gayamin da ta tada rigima kar a auro ku, Allah ba za'a yin ba, dandai bakusan k'ok'arin da baiwar Allahn nan tai muku bane da har ta bari aka auro ku,

"Dan ni 'dinnan da kuke gani, ca nai sam a'a, kada ya 'kara aure, Aysa ta isheshi zaman dunia da 'yan 'yayan su, yace rufa muku asiri zai yi, barin ke Karimatu" inna bilkisu tafadi hakan tana mai nuna da Karimatu, Kafin tace,

"Bazawara ce ke, mijin ki ya miki duka ya sakeki, Allah ya temaka babu rabon 'yaya a tsakin ku, kawun ki ya samu Khaleel da zancen ki, ya rufa miki asiri ya aure ki, Ke kuwa Amina(Yafendo), ta tallan nonon shanu, Allah yai auren ku zai had'u, ta sanadiyyar kad'e 'kanin ki da drivern sa yayi, yaji tausayi bayan an kammala komai, yace xai aure ki ya temakawa Baffan ki da hidimar ku, ganin kunyi yawa awajen sa, amma duk hakan bai isheku yin hankali, kun zauna da abokan zaman ku lapia ba, Sai tada fitina da neman yadda zaku fiddasu daga gidan, Ku na jifansu da sharri da sihiri kala-kala, wanda duk daga 'k'arshe idan da zakuyi nazari kan ku yake dawowa, kukan kurciya jawabi ne, mai hankali ke ganewa. Ko kunsan,

"Hukuncin sihiri, da bokanci da abunda suka 'kunsa? To ku sani baya halatta ga ko marar lapia ya je wajan bokaye da suke ikirarin sanin abubuwan da ke boye, wai don ya gano masa rashin

lafiyansa, kamar yadda baya halatta ya gasganta su cikin abinda su ka bayar da labarin sa ba, domin su suna maganine ko kuma su kirawo aljanu domin su taimaka mu su akan abinda su ke so, to wadannan hukuncinsu shi ne 'kafirci' idan sun yi ikirarin – ilimin gaibi, hakika Muslim ya ruwaito cikin ingantaccan littafinsa, lallai Annabi – tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce;

((من أتى عرافا فسأله عن شيء لم تقبل له صلاة أربعين يوما))

Ma'ana: "Duk Wanda ya je wajan dan'duba sai ya tambaye shi wani abu to ba za'a karbi sallar sa ba ta kwana arba'in". Kuma daga Abuhuraira Allah ya kara masa yarda daga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata agareshi yace:

((من أتى كاهنا فصدقه بما يقول فقد كفر بما أنزل على محمد صلى الله عليه وسلم)).

رواه أبو داود وخره أهل السنن وصححه الحاكم عن النبي صلى الله عليه وسلم بلفظ ((من أتى عرافا أو كاهنا فصدقه بما يقول فقد كفر بما أنزل على محمد صلى الله عليه وسلم)).

"Ma'ana: "Duk wanda ya je wajan boka sai kuma ya gasganta abinda ya ke cewa, to hakika ya kafircewa abinda aka saukarwa Annabi Muhammad tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi". Abu dawud ya ruwaito shi kuma ma'abota littattafan sunnah hudu sun fitar da shi, kuma Hakim ya ingantashi daga Annabi tsirada amincin Allah su tabbata a gareshi da lafazin:
"Duk wanda ya je wuri dan'duba ko boka sai ya gaskanta abinda yake cewa to hakika – ya karficewa abinda aka saukarwa Annabi Muhammad tsira da amincin Allah su tabbata agare shi".
Kuma daga Imran dan Husaini Allah ya karama sa yarda ya ce: Manzon Allah tsirada amincin Allah su tabbata a gareshi ya ce:

((ليس منا من تطير أو تطير له أو تكهن أو تكهن له أو سحر أو سحر له، ومن أتى كاهنا فصدقه بما يقول فقد كفر بما أنزل على محمد ﷺ)). رواه البزار بإسناد جيد

"Ma'ana: "Baya cikimmu duk wanda ya ke yin camfi ko a ke yi masa camfi ko ya yi bokanci ko ake yi ma sa bokanci, ko ya yi sihiri, ko ya sa ayi mishi sihirin, duk kuma wanda ya je wajan boka sai ya gaskantashi a aduk abinda yake cewa to hakika ya kafircewa abinda aka saukarwa Annabi Muhammad tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi". Bazzar ne ya ruwaito shi da Isnadi mai kyau.
" saboda haka ku sani, A cikin wadan nan hadisai masu girma akwai hani game da zuwa wajan 'yan'duba da bokaye da masu sihiri (asiri) da makamantansu, da kuma hukuncin tambayarsu da kuma hukuncin gasganta su da bayanin narkon azaba akan haka. Domin hakika manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya yi hani akan zuwa wajan su da kuma tambayar su da gaskanta su, domin abinda ke cikin haka na muni maigirma da hatsarin da ya ke babba da mumunar makoma kuma domin lallai su makaryatane fajirai, kamar yadda ya ke cikin wad'annan hadisai dana baku, wadannan Hadisai dalili ne cewa boka kafirine da mai sihiri domin su biyun basu cimma manufar su sai ta hanyan yi wa aljanu hidma da bauta musu koma bayan Allah kuma wannan kafurcewa Allah ne da kuma yi masa tarayya – tsarkakken sarki,

“Kuma mai gasganta su cikin abinda su ke cewa na sanin gaibu ya kasance kaman su ne, kuma dukkan wanda ya karbi wadannan al’amura na abinda su ke bayarwa to hakika Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi ya barranta da shi, kuma baya halatta ga musulmi ya yarda da abinda su ke rayawa cewa magani ne. Domin lallai wannan yana daga cikin bokanci da rudar da mutane, kuma wanda ya yarda da hakan to hakika ya taimaka musu akan barnarsu da kafircin su,
Hakanan kuma baya halatta ga wani mutum musulmi ya jewajansu – domin ya tambayesu gameda wanda. Zai aurar da dansa ko wani makusancinsa ko kuma abunda ke iya kasancewa tsakanin ma auratan biyu da danginsu na soyayya da cika alkawari ko kuma kiyayya da rabuwa da makamantan haka;domin wannan yana daga cikin gaibi wanda babu wanda yasansu sai Allah tsarkakke mada’au kaki.

“Kuma sihiri yana daga cikin abubuwa haramtattu na kafirci kamar yanda Allah mai girma dad’au kaka yace cikin sha’anin mala’I kunnan biyu cikin suratul Bakarah: (وَٱتَّبَعُواْ مَا تَتلُواْ ٱلشَّيَطِينُ عَلَى مُلكِ سُلَيمَنَ وَمَا كَفَرَ سُلَيمَنُ وَلَكِنَّ ٱلشَّيَطِينَ كَفَرُواْ يُعَلِّمُونَ ٱلنَّاسَ ٱلسِّحرَ وَمَا أُنزِلَ عَلَى ٱلمَلَكَينِ بِبَابِلَ هَرُوتَ وَمَرُوتَ وَمَا يُعَلِّمَانِ مِن أَحَدٍ حَتَّى يَقُولَا إِنَّمَا نَحنُ فِتنَة فَلَا تَكفُر فَيَتَعَلَّمُونَ مِنهُمَا مَا يُفَرِّقُونَ بِهِ بَينَ ٱلمَرءِ وَزَوجِهِ وَمَا هُم بِضَارِّينَ بِهِ مِن أَحَدٍ إِلَّا بِإِذنِ ٱللَّهِ وَيَتَعَلَّمُونَ مَا يَضُرُّهُم وَلَا يَنفَعُهُم وَلَقَد عَلِمُواْ لَمَنِ ٱشتَرَىهُ مَا لَهُ فِي ٱلأخِرَةِ مِن خَلَق وَلَبِئسَ مَا شَرَواْ بِهِ أَنفُسَهُم لَو كَانُواْ يَعلَمُونَ١٠٢)

Ma’ana: “Kuma basu sanar da kowa ba balle suce: mu fitina kawai ne, saboda haka ka kafirta,” balle har suke rarrabwa tsakanin mutum da matarsa dashi daga gare su. Kuma su (masu yin sihirin) basu zama masu cutar da kowa da shiba, face da iznin Allah. Kuma suna neman ilimin abin da yake cutar da su, kuma baya amfaninsu, kuma lallai ne, sun sani tabbas wanda ya saye shi, baya da wani rabo lahira. Kuma tir da abinda Suka sauar da raukansu da shi, da sun kasance suna sani)). Suratul Bakara, aya ta: 102,

“Sai kuma waccan ayar maigirma da ta yi nuni akan cewa lallai masu sihiri suna raba tsakanin mutum da matarsa. Kamar yadda ta yi nuni kuma cewa lallai sihiri baya tasiri don karan kansa ta fuskar amfanarwa ko cutaruwa, sai dai yana tasiri ne da iznin Allah wan ya riga ya kaddara kuma ya kasantar, domin lallai Allah tsarkakke madaukaki shi ne ya halcci alkhairi da sharri, hakika cutar ta yi girma kuma zaluncin ya yi tsanani ga wadannan masu kirkirar, wadanda su ka gaji wadan nan ilimomi daga mushrikai su ka zo suka rikita masu raunin kwakwale da su, lallai mu daga Allah mu ke kuma lalle mu gare shi zamu koma, Allah ya isar mana kuma madalla da wakili wanda yake shi ne Allah.,

“Ma’aikin Allah ﷺ Ya sake cewa kuma

((من أتى عرافا أو كاهنا فصدقه بما يقول فقد كفر بما أنزل على محمد صلى الله عليه وسلم)).

“Ma’ana: “Duk wanda ya je wajan danduba ko boka sai ya gaskanta shi da abinda ya ke cewa to hakika ya kafircewa abinda aka saukar wa Annabi Muhammad tsira da amincin Allah su tabbata agare shi”.

“Anan zan dakata, ku sani duk wannan ayoyi da hadisai na kawo su ne domin ku, saboda ku

tabbatar abunda kukeyi ba mai kyau bane, babban shirka ne, ko da nan gaba hakan zai zamto silar shiryuwar ku, Ta haka har Allah yasa ku janyo ra'ayin masu hali irin naku, zuwa turbar gaskia. Abunda na fada dai-dai Allah yabamu ladan, kura-kuren dake ciki rabbi yayafe min."

"Ameen..." suka had'a baki d'aya wajen cewar hakan.

Ya Bala da Dr Khaleel ne suka ce da Inna Bilkisu,

"Toh! Inna Allah ya saka da alkhairi, mun 'karu muma gaskia.."

Sannan Ya Bala ya 'kark'are da,

"Toh Karimatu da Aminatu yanzu zamu ji daga bakin shi mai gidan naku kan wane hukunci ya yanke abisa hakan. Domin a zahirin gaskia ni na cire hannuna a harkar ku, babu ruwana, baxan dinga tilastashi ya hakura ba, akan yadda kuke cutar dashi. Saboda haka Khaleel ka yanke hukuncin ka kawai, bansan Inna ba dai, amma ni duk hukuncin da ka yanke, Ina bayan ka, domin sun cancanci kome kayi musu wallahi."

Dr Khaleel ya 'daga kai yana kallon su, Dan murmushin takaici yayi, kafin yace,

"Toh inna ni da na yanke hukuncin sallarmar su kawai, domin baxan iya xama suna cutar da ni da ahali na ba, nan gaba bamusan mai zasu aikata ba."

Wata gigicacciyar 'kara suka saki, cikin zabura Karimatu ta fara sumbatu, Yafendo kuwa rarrafawa tayi ta 'riko 'kafar Inna Bilkisu,

"Inna kiyi hak'uri, mun tuba, ba zamu sake ba wallahi, ni de.. Ni.. dai dama Yaya ce ke sa ni aikata duk wani mummunan aiki, tace idan ba haka ba zata fiddani daga gidan.."

ashar Karimatu ta lailayo ta 'dura mata, kafin kace me? Tuni duk sun to nawa kansu asiri, baram-baram sukai da junan su, kowanne yana kwashe wa 'dan uwan sa albarka. To dama ance komai nisan dare gari zai waye, Allah zai bayyana mai gaskia, a ranar dai gaba d'aya duk wani b'oyayyen al'amari sai da suka bayyana shi, har da yanda aka qullawa Safa makirci. Duk kansu sai suka koma suna hararar junan. Dama haka ne rana dubu ta 'barawo ce, d'aya kuma dal ta mai kaya.

Inna Bilkisu tai hanzarin girgiza kai, kafin cikin dattako tace,

"Kar kai haka Khaleel, nasan kayi hak'uri, kana kanyi ma, karka zamto sauran maza masu saurin yanke hukunci Khaleel, kayi hak'uri ka dubi girman Allah, ka sauqaqa hukuncin da za kai musu, su ci darajar 'ya'yan dake tsakanin ka dasu. Kayi hak'uri Khaleel, mata sunyi yawa yawa agari, yan mata da zawarawa, hakika duk sanda akai saki, al'arshin ubangiji girgiza take, kaga kuwa ba 'karamin abu bane. Kayi hak'uri Khaleelu, Allah ya dubi hakurin da kai, ya cika maka

burikan ka, dunia da lahira, Allah ya muku albarka, ya tsare ku ya ‘kara kareku daga sharrin ma sharranta.”

Sam Dr Khaleel bai so ba, amma ya xaiyi? Hakika zab’in iyaye shine zab’i nagari ba son rai ba. Cikin taushasshiyar murya yace,

“Ameen Inna. Sun ci darajar ki, da wallahi hukuncin da na ‘dauka shine sawwake zaman mu dasu tare, Allah yasa zab’in da kikai shine mafificin alkhairi, na janye qudurina, amma zamana dasu a Abuja ya ‘kare Inna. Ita Karimatu zan mayar da ita can Bauchi inda gidan gona ta yake, ita kuma Amina zata koma jigawa, saboda zan fara part time lecturing acan. Ina ga idan akai haka, komai zai yi sauki, tunda zama waje ‘d’aya shine yakawo had’uwar kan su, dama cusa mummunan ra’ayi a zukatan su.”

Jinjina kai Inna Bilkisu da Ya Bala sukai, alamun sun amince da hakan, Karimatu da Yafendo kuwa sun ‘danji sauki a ransu. A washe-gari kuma aka ‘dakko su Hafsat daga kano, hade da Hidaya dake Zaria. Sosai sun canxa tamkar basu ba, dukkan su, suka rankaya gidan Haj Aysa, takanas daga umarnin Inna Bilkisu wacce ke jagorancin tafiyar. Hak’uri sosai suka shiga bata, tamkar basu Karimatu ba, duk sunyi laushi, fadakarwar da Inna Bilkisu tayi musu, ta matukar canza su, sai dai duk da haka Karimatu da Yafendo sun ‘dau mummunar gaba a tsakanin su, Dan ko d’aya na magana, d’aya bata saka baki. Haka suka dawo gidah, suka kara neman gafarar, Dr Khaleel. Ganin hakanne yasanya Inna Bilkisu baiwa Dr Khaleel shawarar ya ‘dan saiwa su Hafsa da Hidaya matsakaicin gidah kowacce a garin da take aure, saboda zama waje ‘d’aya da kishiya babu dadi. Hakan kuwa akayi, da sati ya zagayo kuma kowacce cikin matan biyu, wato Karimatu da Yafendo, ta koma sabon gidan ta, Karimatu a bauchi. Yafendo kuma a Dutse/Jigawa.

LAGOS IDIROKO.

Bikin Fatima, yayar Saifullah aka yi, aka kaita gidan ta dake port-harcourt. Da sati ya zagayo kuma Islam ta koma Abuja, Don fara lectures din first semester na MBBS.

*USA 🇺🇸 *
Harvard University(Cambridge)

Sosai convocation hall ya cika da students ,parents da kuma teachers. Kowa ka gani da graduation gown a jikin sa, can na hango Saifullah. Sanye cikin graduation gown, tayi matukar amsar jikin sa, ba kadan ba, kyakkyawa r fuskar sa ta kamala ta ‘kara cika da annushuwa. Chancellor ‘din makarantar ne ya kirashi, nan aka bashi award na, best student of the year. Da kuma first call student na department of Architecture. Awards dai kala-kala haka aka dinga kiran sa ana bashi, Muslim student society of Cambridge ma sai da suka bashi award na, Mufti of the year. Kai abun sai sam barka kawai, ba’a cewa komai.

Saifullah faruk muhammad, saurayi ne ‘dan shekara ashirin da takwas a dunia, ya kammala

senior secondary certificate d'insa anan Lagos, inda ya tsallaka nahiyar turai ya karanci fannin architecture a first degree d'insa (Bsc. Architecture), bai dawo ba ya 'dora da degree na biyu a matakin harkar kasuwanci, wato master of business administration (MBA) .

Fari ne, amma ba irin dau 'dinnan ba, kallo d'aya xakai masa kasan Allah yayi kyakkyawar halitta, dogo ne sosai, sannan ba shida jiki, sannan bai cika rama ba, zamu iya kiransa moderate. Yanada yalwataccen gashin kai dana gira, domin girarsa ta kusa had'ewa ma, tsabar cikar ta. Yana da kwantaccen saje a gefan fuskar sa, wanda turawa ke kira sideburns. Idanuwan sa dara-dara ne TubarkAllah. Hancinsa kuwa tamkar shiya zana shi dan tsawo, bakinsa dan 'karami ne jawur dasu kamar ya shafa jambaki. Kai bayyana yadda saifullah yake tamkar bata Lokaci ne, sai dai muce TubarkAllah kawai. Allah yayi halitta.

Yana karbar certificate d'insa yai apartment d'insa, ko takan friends d'insa dake kiran sa bai-biba, domin bayason hayaniya. Shiysa yace su Baba(Uncle Faruk) ba sai sunxo ba ya yafe, burjik ya tadda gifts boxes kala-kala da kati, duk na tayashi murna,

Girgiza kai yayi, shi sam mata suna bashi mamaki, yadda suke gaya masa suna sonshi, ko su rubuto masa wasik'a, yawancin gifts dinma duk sunan 'yammata ne akai. Ko takan su bai-biba ya tattake wanda suka tokare mai bakin 'kofa yai wucewar sa ciki, bakin sa 'dauke da sallama, jefar da gown din yayi a kan sofa, yana sakin siririn tsaki, kafin yace.

"So uncomfortable...!"

Murmushi kawai Islam tayi tana jin dama a fasa auren ta da saifullah ayi da Mus’ab d'in watakila shi zai darajata ya bata mutuncin ta na ‘ya mace. Cikin tunanin data fad’a Riri ta zungure ta, nan suka shiga duba kayan, kusan Riri ce ta d'aukar mata komai, ita Islam kasa zab’a tayi. Sun d'an jima suna hira da Haj Binta kafin su d'auki hanyar gidah. Dai-dai wani joint kafin a k'arasa unguwar su Riri tace su tsaya ta sauka, cikin fushi Islam ta dubeta,

“Haba Riri ai kya bari dai mu koma gidah idan yaso sai ki dawo ke, amma ya za’ai mun fito tare kice a saukeki..” Cikin rashin damuwa Riri tace,

“Toh sakko mu shiga tare.”

Harara Islam ta wurga mata, Riri tai murmushi tana d'aga kafad’a alamun kin yiwa kanki, Malam ubale zai ja mota kenan wani bayarabe ya d'an k'wank'wasa masa motar,

“Megida motanka na hayaki..”

“Subhanallahi ya Allah..”

Cewar Malam Ubale, da sauri suka fito daga motar shi da Islam, Riri dake tsaye a bakin k'ofar wajen ta k'araso tana tambayan Malam ubale,

“Meya faru Malam Ubale?”

“Hajia wallahi banduba ruwa ba, shine take hayaki, Kinga har wata roba tafara narkewa..”

Islam dake gefe ta ja ta tsaya a k'ofar joint d'in tana kamo addu’oi a baki. Riri ta kalli Islam ta gefen ido sosai a firgice take, gashi bata san ta b'ata mata Ap data had’a. Cikin dak’ilewar murya Riri ta cewa Malam Ubale,

“To ya xa’ai kenan yanzu?,Kai ma ka dinga dubawa saboda irin haka.”

“Insha Allahu Hajia..” ya cewa Riri kafin ya d'anje nesa da Islam yana rissinar da kai,

“Hajia bari naje na duba baya ko za’a samu bakanike yazo ya d'an duba mana, ayimin afuwa.”

“Tohm ba komi..”

Shine kawai abunda Islam tace, Riri ta k'arasa wajanta tana cewa,

“Mu shiga ciki to kafin a gama gyarawa.”

“Nanma ya isa..”

Kad’a kai kawai Riri tayi alamun shikenan toh, sannan tasa kai ta shiga cikin joint din, takaici duk ya kama Islam na rashin madafa. Ta juya nan ta juya can, haka taita yi, lokaci zuwa lokaci kuma takan saki tsaki. Cikin haka kuwa wani matashi ya fito daga cikin joint d'in cikin shigar ‘balman’ kayan duk a yayyage wai nan gayu ne, rabin wandon ya zazzago ta baya wanda akewa laqabi da ‘ass down’, gashin kansa kuwa a saisaye yake rabi da rabi sak kan zakara.

Yana tafe yana wak'a, hango Islam dayai yasa shi sakin lallausan murmushi. Nufota yayi gadan-gadan tayi hanzarin mikewa tana ja da baya-baya dashi, saurin riko mayafinta yai taja da karfi da yake k'arfin ba 'daya bane hakan  ya sanya matashin mai suna 4gig k'wace mayafin Islam sai gashi a hannun sa, neman kare jikin ta tashiga yi, shi kuwa 4gig k'ara gigicewa yai ganin siffar Islam. Cikin sumbatu yace,

"Oh baby pls..."

Riri ganin 4gig bai dawo ba yasata fita waje da sauri, ganin yana neman cakumar Islam dake hawaye shab'e-shab'e duk sai Riri ta rud'e sosai ta shiga yiwa 4gig bayanin Islam fa ba 'yar hannu bace, amman kememe yaki bada mayafin Islam d'in, yana ganin bakin ciki Riri ke yi masa dan taga zai shana. Dai-dai Lokacin kuma Saifullah da Abbas sunzo shiga wani gidan kallon ball dake kallon joint d'in dasu Islam suke, kamar ance ya juya idanuwan sa suka mai kyakkyawan tozali da Islam da Riri dama wani gardi a kusa dasu, gardin na k'ok'arin yafawa Islam d'in mayafi ajikin ta, alokacin kuma hak'uri 4gig ya shiga bata ganin dagaske ba 'yar hannun bace bata saba ba, dai-dai lokacin Islam tai murmushin takaici tana kwatar mayafin tana yafawa akanta, Saifullah idanuwan sa suka sake d'akko masa hotan da Islam ke murmushin tana lullube jikin ta da mayafi.

Gaba d'aya sai tunanin sa ya nemi d'aukewa, ashe kallon sokuwa yakewa yarinyar ma gaba d'aya ta zarce tunanin sa. Da kyar yai kwafa yabi bayan Abbas suka shiga cikin gidan kallon ball d'in wanda gaba d'aya hankalin sa na kansu Islam, cikin murya ciki-ciki yace da Abbas,

"Aboki... Can joint din na meye ne?" Abbas dake sipping coke yace,

"Ina fa? Oh wai opposite nan wajen kake nufi? Wani joint ne naga su Dee na zuwa shi da Shambo, Kamar clubbing ne haka ina jin ana d'an shan shisha ne akwai kuma swimming pool awajen."

Jinjina kai Saifullah yayi yana furzar da iskar bakin sa, hakan ya sanya Abbas dafa kafad'ar sa yana tambayar sa lapia, ganin damuwa kwance k'arara akan fuskar Saifullahin.

"Meyasa ka tambaye ni Aboki? Wani abun ka gani ne?"

Saurin kad'a kai Saifullah yayi alamun a'a, yana k'ak'aro murmushin da yafi kuka ciwo, cikin husky voice d'insa yace.

"Bakomi Aboki, kawai ina mamakin yawan irin guraren nan a Lagos ne, gaskiya sunyi yawa, barin ma dai area d'innan, so suffocating."

Haka dai suka shiga wata hirar da Abbas, can waje kuwa 4gig sosai ya k'ara bawa Islam hak'uri kan abinda ya faru, Riri ma ta k'ara bata, da kyar Ubale ya samo mechanics suka gyara motar, sannan yaja su suka tafi ciki harda Riri da taji baxata iya zama ba acan. Saifullah daya koma

gidah kuwa sakawa da warewa ya shiga yi, yarinyar nan dama haka take? ya ‘dauka son aure da nacin sai taxama matar sa shine burin ta, ashe ashe mizanin tunanin sa kad’an ya d’ebo akanta, harda harkar maza take bi kenan?

“Subhanallah ya Allah..”

Ya furta yana mai dafe da kansa sabida yadda yake sara masa yana barazanar fad'owa. A daren bai kwanta ba sai da ya yanke babban hukunci da zai aiwatar akan Islam inda sukai aure. Islam baiwar Allah kuka sosai ta shiga yi a sujjadarta, tana neman yafiyar ubangiji abisa abinda ya faru d'azu. Nan jikin Riri yayi sanyi lokaci d’aya itama ta mike ta shiga band'aki ta d'auro alwala ta shiga jera salloli..

Shirye-shiryen biki ake yi ganga-ganga daga duk b'angare biyun, nasu Islam dama na d’aya amarya wato Dr Teema, ango Khaled kuwa duk ya matsu so yake kawai a d'aura aure a damka masa matar sa su ware subar k'asar domin visa da yake jira ta fito, kai kace a gidan rik’o yake gaba d’aya tamkar wanda yake akan k'aya haka ya k’agu su bashi amaryar sa, shi kuwa miskilin sarkin fad’in rai wato auta saifullah kuwa, sai abinda aka tilasta shi yayi shi yake, domin abokan sa sun yi shirye-shirye sun shirya lafiyayyar liyafar barbecue yace babu inda xashi, k’arshe dai sai ‘kawayen Islam ne da abokanan nasa sukaje aka d'an gwangwaje duk da ba haka aka so ba.

Da misalin k'arfe sha biyu 12:00pm jirgin 'yan tafiya kano daga Abuja ya sauka a filin jirgin malam Aminu kano dake kano. Kowa kagani sai murna yake da wannan babban budiri da za'ai, 'yan d'aurin aure ne suka fara zuwa inda aka d'aura auren Fatima Muhammad wacce ake kira da Dr Teemah, da angonta Khaled Mommodu Mele, akan sadaki dubu d'ari biyu cif. Dubban mutane ne suka shaida hakan inda da rana mahaifiyar amaryar wato hajia Fareedah Muhammad Abbas ta shirya had'add'iyar liyafa wadda ake kira da mother's Eve. Taro yayi taro, anci an gyatse 'yan uwa duk sunxo kano,

B'angaren su amarya Islam kuwa k'awayen ta na BNA dama na Nile sune suka had’a mata d'an event d'insu na k'awaye na ‘bridal tea party’ , Amarya Islam tayi kyau ba k'arya inda Mamza Beauty ta tsantsare mata kwalliya, kayanta kuwa Hudayya Fadoul ce ta d'inka, gayawa mai karatu irin had'uwar da Islam tayi b'ata Lokaci ne, domin kunsan yadda prof Khaleel yake san Islam da ma Ya Bala, uwa uba autar mata ce, gata ta gaban goshin mahaifiyar Saifullah.

Washe garin safiyar Asabar da misalin k'arfe biyu na rana aka d'aura auren Saifullah Faruk Muhammad da amaryar sa Bilkisu Khaleel Muhammad (Islam) akan sadaki sisin gwal guda d'ari biyu cif, A masallacin central mosque dake Abujan. Domin mahaifin Saifullah yace tunda dai Islam ta had’a zuri’a da kanuri babu abunda zai hanashi yi mata irin al’adar su. Daganan aka yi reception d'an gaske domin anci ansha, ango yayi shiga cikin dakakkiyar getzna kalar sararin samaniya ya d'ora hula zanna bukar gashi yasha takalmin sa batozzi sau ciki dark blue, agogon hannun sa na azurfa da zobe da suka amsa sunan su, kallo d’aya xakai masa ka furta kalmar ‘TubarkAllah’. Duk inda yayi masu hoto na binsa, sai murmushi yake yi kai kace auren soyayya

ne.

Cikin takun k'asaita yake tafiya, daga nan suka koma gidah shi da abokan sa yin wanka na biyu dan zuwa gidan su Islam, kafin anjima suje liyafar gidan su Islam d'in da aka shirya ta 'wushe-wushe'. Domin hatta kayan da zai saka komai irin na al'adar ne, shi abun har mamaki Maman ke bashi ganin yadda take komai a tsare sai kace akansa ta fara aurarwa.

Islam kuwa na can tana kuka, tunda akace an d'aura auren take hawaye domin tasan babu wanda ya isa ya yanke wannan k'addararren auren dole da Allah yayi sai anyi shi. Da kyar tadaina kuka ta koma ajiyar zucia. Hafsat da Hidaya dake gefe kuwa murna suke mata ganin ita kam ta tsallake sirad'in auren sa'annin daddy, zata auri sabon jini uwa uba kuma yaro matashi mai jini a jika. Duk sun wani yamushe duk da yanzu ba laipi suna samun kulawa, amma ba kamar suna gidah ba, domin sai kace wanda sukai shekara goma a gidan aure. Hidaya duk ta yi laushi, Hafsat kuwa idan ba dole ba yanzu bata fiye magana ba, domin dunia ta koya mata hankali. Cikin taushasshiyar murya tace,

"Uhm! Islam ba kuka ya kamata kiyi ba, alwala zaki d'auro kiyi sallah ki godewa Allah ya azurtaki da wannan babbar kyautar.."

Hidaya dake gefe tai murmushi tana jinjina kai kafin tace.

"Wallahi kuwa Hafsat, yanzu da ace ba muyi wasa da rayuwar mu mun cuci kanmu ba, ai da muma samarin kila zamu aura, amma dubemu Islam, ko ba kya son mutumin nan karki tab'a nuna masa da sannu zaki so shi, ki kuma kyauta ta masa sai kiga Allah ya dube ki da idanun rahama yasa ya mato akan ki."

Islam dake gefe ta dube su kawai tana d'auke kanta, kafin cikin sark'ewar murya tace.

"Ba zaku gane ba, baya so na shima yana min kallon wata k'ask'antacciya, fisabilillahi meye nawa aciki? Wallahi bansan anzo an nema masa aure na ba sai da Yayya Yakolo take fad'a min... ku.." Hafsat ta katseta tana mikewa tsaye, cikin fushi tace,

"Islam ya kamata ace ni da Hidaya mun isheki ishara, kalli yanzu ni wanda aka aura min mai mata biyu fa, daga shi har matan nasa sun haife ni. Kai 'ya'yan sama sun mugun girme mini." Hidaya dake gefe ta amshe da,

"Ba gwara ke ba Hafsat, ni fa matan sa uku ni ce ta hud'u, ko a mafarki ban tab'a zaton hakan zata kasance dani ba, sai gashi wanda ya girmewa mahaifi na shine ya zamto mijina, harda rabon d'ansa ko 'yar sa gashi a k'unshe a marata. Amma Alhamdulillah kukan kurciya jawabi ne ga mai hankali, Tabbas abubuwan da mukai na laipi ada shine muke girbesu yanzu. Fatanmu Allah ya k'ara karb'ar tubanmu yasa hakan shine mafificin alkhairi"

"Ameen.."

Suka fad'a baki d’ayan su, zumbur Hafsat ta mike ta fita daga dakin da alama ta tuno mahaifiyar ta, maganganun da sukai ya taso mata da zaman mahaifiyarta Karimatu a baya. Nan Hidaya ta shiga baiwa Islam shawarwari na irin yadda zatai zamantakewar gidan aure da sauran su. Sun jima kafin Yakolo ta shiga d'akin ta tasa keyar Islam su koma sama.

Wani ruwa mai tashin k'amshi a babban baho Yakolo tasa Islam agaba ta cire kayanta ta shiga ciki, bayan ta fito daga ciki ta sake turarata da wani turaren wuta na jiki, kafin a d'akko mata wasu kaya da sukai kwana da kwanaki ana turararasu a kabbasa. Lungu da sak’o na jikin ta sai da aka shafeta da wasu irin turaruka.. (sirri ne tawan (billyn Abdul) tace karna soma fad'a muku).

Wani arnen komole lace royal blue ta saka mai kwalliyar golden, tasha adon gold hatta mayafinta da takalmin duk Golden ne, ba kad'an ba Islam tayi kyau ga wani sihirtacce kuma ni’imtaccen k'amshi da yake tashi daga jikin ta na shuwa-shuwa-yerwa fato-Chadians, kai duk ita d’aya dai akai mata wannan combo. Light makeup Lee tayi mata, sannan takama hannunta suka sauka k'asa wajen angwaye inda Saifullah ya wani hakimce a zaune yana danna waya.

Ta k'asa-k'asan ido yake duban su Islam dake sakkowa, baki da hanci harda idanuwa haka Saifullah ya baje yana kallon Islam.. ‘Fata barakAllahu ahasanul khaliqeen.’ Shine abinda ya furta ba tare da yasan yayi ba daman k'asa-k'asa ya fad'a yana neman sai-saita kansa, sai yanzu ya lura yarinyar bayan jiki mekyau tana da wani irin sihirtaccen kyau sosai. Ya dubi abokansa yaga yadda suka zuba mata idanu gaba d’aya sai yaji haushi ya kama shi kuma.

Cikin takun sa na isa ya k'arasa ya fincikota zuwa jikin sa, kirjinta ya manna a nasa, take yaji tsigar jikin sa na tashi yarrrr, itama mutuniyar taku anata b'angaran hakan ne ya faru. Cikin rad’a-rad’a kamar irin soyewar nan suke yi ya shiga yi mata magana a hankali kamar zai lashe mata kunnen, gaba d’aya kamshin jikin ta narkar dashi suka yi, k'ok'ari kawai yake yi ganin bai yi wani abun da zai sa a gane yanayin da ya shiga, gashi abokansa da kawayen ta sai tafa hannuwa suke a lamun ya burgesu domin yadda suka yi irin na masoyan nan ne,

“Sam baki yi kyau ba malama... Ga wani kaurin turare dake tashi a jikin ki so suffocating.” Shine abinda Saifullah yake gayawa Islam a cikin kunne gashi ya nanuke ta danma dai ta zama tasa yanzu. Mutsu-mutsun kwace kanta take yi ya sake rad’a mata cewar,

“Don’t you dare create a shameless scene here, abokai na masu class ne basu zubar da nasu ba kamar yadda kika zubar da naki a titi. So karki bawa kanki kunya a gabansu fatana Allah ya shiryeki.”

Yana fad'a ransa na k'ara jagulewa tunowa da yai da ranar da daya gansu da 4gig a joint, mayafinta a hannun gardi tana sakin murmushi. Saurin tunkud’eta gefe yayi yadda ba kowanne zai gane ba sai ita, murmushin takaici tayi ta shiga gaishe da abokan ango, sunata tsokanar ta aka shiga d'aukar hotuna, Saifullah na k'ak'ume da hannun Islam kamar gaske, mintuna kad’an

ya juya ya gasa mata bak’ar magana a kunne. Duk Islam a takure take dan haka suna tafia taji dad’i a ranta, nan ta koma cikin 'yan uwa aka cigaba da shewa lokaci zuwa lokaci maganganun saifullah na mata yawo a zuciya suna kuma susar ta idan ta tuna kalamansa.

“Wai na zubar da class d'ina a titi, toh mai yake nufi da ina yi kenan?! Ya Allah”

Haka Islam ke fad'a a hankali idanuwanta sun ciko da hawaye, da wannan su Yayya Yaburra suka sake d'aukar ragamar shirya Islam don zuwa wushe-wushe, an yarfa mata 'kela yaske’ (kitson gaba), gana lalle baki da ja, kamshi ta ko'ina tashi yake daga jikin ta, ita dai Haj Aysa nata idanuwa ne kawai domin duk k'annenta sunyi kanai-kanai akan komai, wani dandatsetsen cotton lace ta sanya aka nad’a mata laffaya wadda taci sunan ta 'yar gaske, komai na al’adar kanuri tasa, sarkar k'afa data kai ga kuma b'ular hancinta tasha ado da ‘yar barima itama, komai dai tsab abun ba’a magana sai dai a ce tubarkAllah kawai.

K'arfe bakwai aka fara tafiya wushe-wushe ango Saifullah shima yasha shiga cikin komai na al’adar barebari, ba kad'an ba yayi kyau, abokan sa sunsha ado suma, k'awayen Islam ma sunci ado cikin dangashe da mandil peach color, 'yan uwa kuma sun sa blue and black. A convoy suka tafi inda xa’a gudanar da sha’anin. Motar Saifullah da Amarya Islam itace a k’arshe, tunda ta shiga cikin motar yake kallonta ta gefen idonsa, ba kad'an ba tayi masa kyau, amma abunda ya dasawa zuciyar sa akanta ba zai iya furta komai ba. A haka suka k'arasa inda za’a gudanar da event d'in,

Sai bayan kowa ya shiga mc tai announcing shigowar couples SAIFUL_ISLAM, a tare suka shiga hannun su sarke dana juna, da abokan su dake binsu a baya mace d'aya namiji d'aya suna bin taken gangaa kura kowanensu yasha kitson gaba abindai sai sam barka kawai... Can baya kuma 'yan uwa ne su Yakolo, Yaburra da sauran ahalin prof Khaleel. Tuni aka fara xubawa makad'an gangaa kura yirne, waje kuwa jin kid'a yana tashi yasa aka fara sakin al’adar durum kageye, su kaka deeja kuwa sa bada nagaya ka ajiye suke(turaren wuta).

Riri ce ta bada tarihin amarya inda take cewa.

"Amaryar mu dai ta kasance 'yar autar mata a wajan iyayenta, sannan tana da kuka dan duk abinda aka yi mata ko hararta aka yi, Sai tayi kuka dan haka ango sai ka kiyaye dan karka ce ba'a sanar da kai ba, sannan amarya tana da hakuri uwa uba kawar da kai akan abinda duk ba'a sanyota a ciki ba, tana da ilimin ta dai-dai gwargwado na arabi dana zamani, sannan akwai shagwab'a, ga karatun novel’s da son girki, My bestfren is amazing to the extend that no word could describe how sweet she's. Ga 'kamshi malam, Angonmu xaka sha 'kamshi. dan haka ango Saif sai ka shirya dan wasu abubuwan sirri ne sai kunyi aure zaka binciko su.' May your new home be forever blessed.”

Gabaki d'aya gurin babu wanda bai yi dariya ba, shi kansa Saifullah banda yana jin haushinta yaso ya dara sai kuma yayi ta maza ya basar. Riri na komawa wajan zamanta Abbas ya taso wanda shine zai bada tarihin ango, yana sosa saman hancinsa yace.

"Kowa dai daga gani yasan angon nan ba baya ba, shalele ne d'an gata d'an auta kuma d'an gayu. Ni abu na farko da zan bawa amarya shawara akai shine, kiyi ta hakuri domin kuwa mijin nan naki akwai 'yan mata gashi sune suke kai masa hari, abinda zance dake shine kisan yadda zaki wajan kama zuciyarsa ya zamo naki ke kad'ai. Sannan Saifullah yana da hakuri wanda ba kowa zai shaida hakan ba sai wad'anda suka zauna dashi, Toh Aboki na dai miskili ne gaskia, mr arrogant ba hehe, amma azahirin gaskia he's fun to be with, Saboda bestie na komai yanada time awajen sa, yace time dinsa is priceless. Amma amaryar mu kinyi sa'a saboda saif is kind, attentive and most caring wlh.. sannan lastly Kiyi hak'uri da addicted kalmar sa ta kullum wato so suffocating. Nima dai a karshe zance amarya ba zata gama sanin waye ta aura ba sai sun fara rayuwa, Allah bada zaman lafiya ya kawo kazantar d'aki bata sharaba ta...."

Saifullah kuwa cikin makoshi ya furta,
"So suffocating"

Gabaki daya gurin sai ya hargetse da surutu, wasu suce Allah sarki Islam wasu kuma suce ai itama tana da kyau wasu suce idan ta kama wata na soyayya da mijinta taci kaniyarta, da alama dai Abbas yabar gutsiri tsoma a wajan yayin da shi kuma yana gefe yana bankar dariya harda rike ciki.

Amarya Islam na dosar tsakiyar fili wace jikinta ya kuma yin sanyi jin yadda mijinta yake, aka canxa waka xuwa na shuwas wato can dangin mahaifiyar su baban Saifullah, wakokin khamal yaqub/mansur ne ke ta tashi dana Amina rawaram.. Islam na xama aka fara gudanar da al'ada, komai a tsare Saifullah da Islam sai magana suke a hankali, kai kace hira suke yi, amman ina warning yake korawa Islam kan tacigaba da acting it suits her, idan ta nuna akwai wani abu a tsakanin su, sai ya dizgata a gutin ita kuwa cewa take ya kyaleta, yana kara damke hannuwanta har wani lumshe idanu yake.

Anci ansha ankuma gyatse, can na hango 'yan Saiful_Islam fans group da home of novels suna lafta loma, idanuwa hud'u mukai da rano dake saye kisre tana dannawa a nursing bag d'in affan girgiza kai kawai nai don tasaba, Can gefen Hall kuwa rano Online novels ne da ya hajja ce novels keta lomar abinci, excellent writers members ma can na hangosu irin su nafee anker da didi sai danna snacks suke a jaka..

Cikin basarwa nace wa Ya Hajja dake gefe "Gaskia k'awayen Billyn nan (billyn Abdul) basu hadu ba, kallesu suna yarfa mu a idanun mutane." dota billy s fari dake gefe taja tagumi tana cewa, "wallahi Mom sai a hankali kam, mu tafi kawai so uncomfortable."🤟🏽

Washe gari akai English party wanda su Ya Safa suka had'a. Daganan akai bud'an kai da safe a gidan su Saifullah dake Abuja, Saboda rankatakaf k'wansu da kwarkwatar su tun biki na sati hudu suka dawo Abuja da xama, hadadd'en gidah mai kyau na mace d'aya sama da k'asa Alhaji Faruk mahaifin Saifullah yabasu kyauta su zauna shida matar sa, anan unguwar Asokoro. Tunda aka fara maganar kaita gidan ta Islam take kuka mai tsuma zuciyar duk wanda yake

sauraro.

_kunji shiru kwana biyu ko? Wlh rasuwa akayi mun, Banda nutsuwar typing shiyasa. Thanks for the messages and call. Allah ya bar zumunci💕_

_WRITTEN BY THE ELOQUENT WRITER:MISS XOXO🧕🏼_

[1/3, 10:53 PM] Miss Xoxo: *_SAIFUL_ISLAM...💕*_

*_NA*_

_*©NANA HAFSAAT*_
*_(MISS XOXO)*_

_*®HASKE WRITERS ASSO.💡_*

*_SADAUKARWA GA:*_
_ASY KHALEEL💕_

*_TUKWICI NE GARE KU:*_
_YA HAJJAH CE😻_
_BILLYN ABDUL😘_

*_SHAFI NA 46-49_*

_SHAFIN YAU NA KI NE MYRIAM💕FATAN ALKHAIRI AGARE KI TAWAJE NA🌹ALLAH YA BIYA MAKI BUKATINKI NA ALKHAIRI, KUMAO🤟🏼_

_nanahafsat.wordpress.com_

Nannauyar ajiyar zucia Islam ta sauke bayan fitar Saifullah. Sai raba idanuwa take yi. Dakyar ta iya jan sayyadar ta, tashiga ‘bandaki, alwala tayo tayi sallah, ta bude drawer dinta da su Yakolo suka shirya mata kaya, riga da wando kakkaura ta ‘dakko ta saka. Tabi lapiar gado, Don dama

tayi sallah d’axu. Wayar ta, ta ‘dakko ta shiga WhatsApp, messages rututu tagani ana tayata murna da Allah yasanya alkhairi. WhatsApp family group ‘dinsu ma na ‘Y’ar Gaya Fam Bam’ duk maganar bikin ake yi, sai na secondary school dinsu na BNA 2k14. Shima sai yad’a zancen akeyi, ita dai dariya kawai takeyi, sannan ta turawa kowanne grp emijo na love ❤. Nan aka shiga maganar ‘ya amarya da yin reply,ina ango,’

“Yana gaida ku, sai da safe..”

Tacewa kowannen su, kafin ta kashe data dinta ta kwanta, ko takan reply din Lee dake cewa ‘sai tazo gashin amarya da safe’ bata bi ba, nannauyan bacci lokaci d’aya yai awun gaba da ita. Da asubah ta mike jin kiran sallan masallacin mak’otansu, hawaye ne ya ciko fal idanunta na ganin dagske dai tabar gidah har abada, kiran sallar ma ba ‘daya bane, Ta furta aranta.

Bandaki ta fad’a, tayo wanka had’e da alwala, sallah tayi da azkhar. Kafin ta dakko littafin anatomy tashiga karantawa, haka wani baccin gajiyar ya sake awun gaba da ita akan sallayar sallan. Saifullah kuwa da kyar ya tashi yana murza idanu, bandaki ya shiga yana had’a hanya don bacci ne fal idanun sa, ya sakarwa kansa shower. Sai da ya fitar da baccin daga idanun sa, sannan ya ‘dauro alwala ya fito ya zira jallabiya ya fita masallaci, ana idarwa kuwa ya shiga bakinsa dauke da adduar shiga gidah,Kamar ya shiga ‘dakin da Islam take sai kuma ya fasa yana haurawa sama abunsa, wayar sa ya janyo yana duba time table d’insa, ‘jogging time’ shine abunda yakamata yayi a lokacin. Kayan exercise dinsa ya ‘dakko yana feshesu da turare, sannan ya zura su ya fice motsa jikin daya saba. Haka yai ta jogging har takwas saura kafin ya koma a matukar gajiye, ya bude gidan don ba’a kawo musu mai gadi ba tukun.

Lokacin kuma Islam ta gama turara kayanta akan kabbasa, dinkin riga da skirt, cikin dakakkiyar atamfa Holland, pusher pink and black color, mai zanen agogo. Ta gyara ‘dakin duk da ba wani datti yai ba, haka ta karkad’e ko’ina tana yaba tsarin gidan. Ba kadan ba yayi mata kyau, sosai kayan da aka zuba sun ‘kara ‘kayatar dashi. Simple ‘dauri tayi ta fito hannunta rike da burners guda biyu da ledar magic coal, ta jona burner ‘d’aya a corridor ta zuba turaren halut, a parlorn ‘kasa kuma ta jona ‘d’aya ta zuba ‘sandal bange’. Kitchen ta nufa da ledar magic coal a hannunta tana yaba tsaruwar kalar kitchen cabinets din, domin orange and black ne, sai kitchen utensils kuma duk silver color aka zuba mata, santin komai take yi tana shi wa iyayenta albarka. Nan da nan ta kunna gas ta dora coal igniter ta kunna coal biyar aciki, suna kamawa ta zuba a kasko, tuni ta barbad’e shi da turaren wutar Hawi. Jama’a gidah dai ya tashi da ‘kamshi kala kala, ba a magana kawai, Ga na jikin ta dake tashin turaren kaya dana khumrah’s.

Heater ta jona, ta ‘dora ruwan zafi na tea. Don taga komai akwai shi wadatacce a kitchen din, domin store dinma shak’e yake da kayan gara, tea yana tafasa ta juye a royal flask dinta ta kai kan dinning ta’ajiye. Ajiyewar ta yayi dai-dai da shigar Saifullah parlorn, bakin sa ‘dauke da sallama. Amsa masa Islam tayi duk a rud’e take. Tunowa da jawabin Inna Bilkisu datai hakan yasanya ta hanzarin tsugunnawa, cikin siririyar muryar ta tace,

“Ina kwana?!”

Tabe baki Saifullah yayi, bayan yagama kalleta sama da ‘kasa, ga ‘kamshi na dukan hancin sa na jikin ta da turarukhan wutan, cikin turo baki gaba yace,

“Yana kwano.”

“Me za’a dafa maka?” Cewar Islam, kanta a ‘kasa..

Ware idanuwa Saifullah yayi, yana mata kallon renin hankali kafin yace,

“Ni zaki dafawa abinci?! Lalle ma yarinyar nan.”

Yana gama fad’a ya haura sama abunsa, tab’e baki Islam tayi, ta koma kitchen, cikin minti biyar ta kammala dafa indomie d’aya had’e da soyayyen kwai guda biyu. Daki ta koma abin ta, tana ci, sannan ta koma kitchen ta wanke duk abunda ta ‘bata. Ta zauna a palor tana tunanin cakwakiyar zaman da xasuyi da Saifullah. Tana jiyo ‘burin ‘burin ‘dinsa a kitchen din sama. Ashe coffee ya had’a a coffee machine. Sai tara dai-dai aka kawo musu abinci daga gidan su Saifullah, Fatma da Humaira ne suka kawo, sai tsokanar ta sukeyi itadai murmushi kawai take. Cikin haka kuwa Saifullah ya sakko, sanye cikin dakakkiyar shadda galila golden datasha aikin hannu milk color, hular sa a hannu milk color yana gyara karin ta, Kallo ‘daya yai musu dukkan su ya maida kansa kan hular sa, Fatima yayar sa ta mike tsaye tana nufar inda yake,

“Autan mu..”

“Ya fati..”

“Na’am Auta, yauwa ga abinci can aunty tace akawo muku, naga amaryar mu ma har da wahala, tayi tea gashi can a dining.”

“Tohm angode”

Cewar Saifullah, Humaira dake gefe tace,

“Ya Saif ina kwana?”

“Humaira..” abunda yace kenan kawai ya sa kai zai fice, Fatima ta riko rigar sa,

“Ina zaka ango da sanyin safiyar nan? Indan mune dawo ka zauna, yanzu zamu tafi. Dama sallama nazo muku yau zamu koma mu.”

Ware idanuwa Saifullah yayi, cikin sauri yace,

“Komawa kuma?! So soon haka? Amma banda Mami ko?”

“Duk ‘yan lagos yau kowa zai tafi bare ni da ke port-harcourt,k..”

Ai be jira ta gama ba ya fice cikin sauri, Islam dai duk tana jinsu bata tanka ba, nata dai murmushi ne kawai, Fatima da Humaira suka shiga hirar su, lokaci zuwa lokaci islam ke samu su baki, sam kunya take ji, haka kawai taji har Humairan take kunya, uwa uba kuma Fatima yayar Saifullah.

A ‘dari Saifullah ya figi motar sa, sai gidan su, yana zuwa ya tarar kuwa yan uwa nata shirin tafiya, duk sai yake jin ba dadi, haka dai ya amsa gaisuwar kowa awajen a kunyace musanman yadda suke tsokanar sa, ‘dakin Haj Zuwairah ya nufa, lokacin ta fito kenan daga kitchen hannunta rike da kofi da kunun tsamiya aciki. Fad’ada murmushin ta tayi, tana karasawa cikin dakin.

“First love..” cewar Saifullah,cikin shagwababbiyar murya.

“Auta na.. kadde kace su Fatima ba su kai muku abincin ba, yau naji shirme a wajen yaran nan.”

“No sun kai.. Ni first love zuwa nai wajen ki, I love and miss you, dakyar nai bacci jia” ya karasa fada yana dora kansa a cinyar ta.

“Shine ka baro yarinyar mutane acan? Ni auta yaushe zaka san ka girma ne? Tashi ka tafi”

Make kafad’a ya shiga yi, yana jijjiga kansa alamun a’a. Cikin cuno baki yace,

“Ni fa first love kinsan inde ba siblings dina ba da ku, da sauran family i barely eat with strangers.”

Salati Haj Zuwairah ta rafka tana ‘daga kansa daga cinyar ta,

“Wacace stranger auta? Islam matar taka ce ta koma bare kuma? To tashi tun muna shaida juna ni da kai ka tafi gidan ka, ko na mugun sab’a maka. Akan yarinyar nan Allah auta zamu ‘bata dakai, ka kasa sakin jikin ka da ita, kar dai kacemin kana mata wannan halin naka itama.”

Cikin cuno baki gaba yace,

“First love, Ya Fati ce fa tace yau zaku tafi..”

“Sai akai yaya da tafiyar mu? kai fa nace ka kwantar da hankalin ka, Baban ku yace zamu dawo muma nan ‘din cikin shekaran nan, to menene abun damuwa kuma uhm?”

Shiru Saifullah yayi, gaba d’aya tamkar zaiyi kuka haka fuskar sa ta koma, ganin hakan

yasanya Haj Zuwairah, tausar sa, don tasan halin autan nata baya cin abinci sai ta tasa shi agaba, kamar yaro, bayason abinci, yawanci sai abu mai ruwa-ruwa, kuma bana ko'ina yake ci ba, sai na gida, Sam bayason na roadside ko na wasu restaurants din. Abincin ta zubo masa, da kunu sai da yaci sosai, sannan ta tasa 'keyar sa suka tafi, dama tayi niyar zuwa ta gano gidan daganan ta musu sallama, fal suka cika motoci uku, sukaje gidan . Lokacin itama Islam yan uwan Ammi sunzo fal na bornu suma duk yau zasu juya hakama na 'yan 'kauyen y'ar gaya. Tuni gidan ya kacame, Ita dai Islam na dakinta tana canza wani kayan, domin tayo wanka na biyu. Ta shirya cikin wani lace ja, doguwar rigar A shape, hannun kuma peplums akai masa. Ba kadan ba tayi kyau. Light makeup Lee keyi mata,

"Lam Lam ba ki labarta mun first night ba.."

Dariarta Islam ta danne, ko da hakan ta kasance ai ba zata tab'a fada ba domin Yayya Safa tace karta soma bawa kowa labarin yadda sukai auratayya da mijin ta, dama duk wani sirri dake tsakanin su, don babu kyau. Murmushi tayi kafin tace,

"Bari kawai, ba'a magana it's beyond your imagination, ki shirya hajjaju.."

Lee ta bude baki, ganin da gaske labarin da take ji akan hakan ashe gaskia ne, Yatsina fuska Lee tayi kafin tace.

"Tab zan iya yadda kuwa?"

"Da me fa" cewar Islam, cikin zakuwar abunda Lee zata fada.

"Wallahi ina gaya miki, Fahad ya matsa shi aure kwanannan, Naga abun nasa na neman zautar dashi nace yafadawa Baba sunfi kusa, shine jiya yake cemin cikin satin nan za'a kawo komai, kuma biki bayaso ya wuce nan da wata 'daya."

Cikin murna Islam tace,

"And so?! Kakki wani damu wallahi, Allah yasa hakanne yafi alkhairi, mu gwangwaje mu rak'ashe."

"Waye zai barki ki rak'ashe ki gwangwaje? Lokacin ma akwai little unborn, beside Ya Saif baze yarda ba"

Tab'e baki Islam tayi, cikin cuno baki tace,

"To y'ar ciki baki, sai ki hana ai.."

"That aside.. Ni kuwa kinji labarin cousin d'inki Saifullahi, zai fara lecturing a school namu ko, as visiting lecturer amma, shi zai 'dauki course 'din: Introduction to Humanities and community

medicine"

Tabe baki Islam tayi, kafin tace,
"Lalle, Za'a sha ruwan carryovers"

Lee ta kyalkyale da daria kafin tace,
"Kiji tsoron Allah Lam-Lam, dan jinin ku bai hadu ba sai ki laqaba masa sharri, in sha Allah zamuyi passing kowanne course with flying colors.."

Islam ta mike tana kallon kanta a wani mudubi, dogo fari kal, kana kallon kanka full dnka ta ciki. Ba kadan ba ta yaba kwalliyar da Lee ta mata, ta faffesa perfumes kafin tace,

"Can ta matse muku ke da shi, yanzu dai tayani kwaso ledojin nan, Ammi tace na babbawa duk wanda sukazo zasu tafi.."

Kad'a kai Lee tayi, tana duban ledojin, atamfa ce guda d'aya, da kwalba cike da turaren wuta, sai kasko da hair dryer set a kowacce leda, kin kima sukai, suka kai parlor, Islam duk ta takure da irin shegen kallon da Saifullah ke jefanta dashi, in sun had'a ido kuma ya sakar mata harara, ita abunma daria yake bata.

'Y'ar walima dai akai na yan uwa da suka zazzo, yan bornu ne suka fara yi mata sallama suka tafi, ta bisu da ledojin su, daga nan yan Y'ar gaya suka 'daga suma, bayan sun tafi da awa d'aya su Haj Zuwairah suka fara mikewa don tafiya, Saifullah yayi rau-rau da idanuwa kamar zai yi kuka, sosai 'yan autancin suka motsa masa, sai da Haj Zuwairah ta tasa 'keyar sa 'daki, daga shi har Islam din ta sasu agaba, ta dubi Saifullah tana murmushi kafin tace,

"Haba auta, ai sai matar taka ta rena ka, 'katoto dakai zakai kuka"

Ai kuwa daria ta tahowa Islam ta gimtse ta dakyar, Nan de Haj Zuwairah ta shiga yi musu nasiha da jan hankali na yadda zasu gina rayuwar auren su, ta 'kark'are da,

"Wannan sabuwar rayuwa ce kuka shige ta, wadda ba irin ta baya bace, sai kunyi hak'uri da juriya akan komai, ga ku duk 'yan auta, ni dai auta ga amanar Islam nan, kaga itace karama dan Allah ko menene zatai maka kayi hak'uri, komai 'dan hak'uri ne, ke kuma Islam ki bishi sau da 'kafa, karki bi zugar 'kawaye ko shawarar su wurin munanta masa, yi nayi bari na bari, nasan Auta na jan ido ne sai da magani, sai kina hak'uri dashi, amma idan ki kai hak'uri zaki ga ribar sa, domin shi mutum ne mai saukin kai, Allah ya muku albarka..Duk abunda kike bukata ki gayamin kinji auta ta?"

Murmushi Islam tayi tana rufe fuska jin itama ana kiranta da auta, Mami tai daria kawai kafin tace,

"Sai maganar abinci, sai kin matsa masa bayason abinci, tun yana 'karami muke fama, ungo

nan, lists ne na duk abunda yake ci.” Ta karashe maganar tana mika mata wata takarda, kafin ta sake cewa,

“Kema ki dinga cin abinci kinji auta ta, duk abunda kike so kici ki girka kinji, idan an kawo miki y’ar aiki ma sai ta dinga tayaki da wasu abubuwan, Allah ya muku albarka..”

“Ameen..” suka amsa gaba ki d’aya.

Dakyar dai Saifullah ya bari su Haj Zuwairah suka tafi, har ‘dan zazzabi yai, domin duk dunia yafison mahaifiyar sa, ya shaku da ita fiye da komai, bai tab’a soyayya ba, bai san ya ake yi ba, domin duk ‘yammatan dake nuna suna sonsa ba ya taba basu fuska, ya ‘dauki mata marassa kamin kai, aganinsa duk haka mata suke, domin yadda suke farautar zuciar sa abun har mamaki yake bashi, shiysa ya jingine kalmar So gaba d’ayanta ballantana soyayyar kanta. Shi kadai yake rayuwar sa, ko kadan bai taba sawa a zuciar sa, zai yi soyayya ba bare aure nan kusa ba ma, sai gashi rana tsaka anyi mai auren dole. Auren dolen ma da yarinyar dake rokar maza su aure ta, take kuma zubar da mutuncin ta a titi....

Haka dai rayuwar gidan *SAIFUL_ISLAM*, ta cigaba. Kowannen su harkar gaban sa yake, gwara ma Islam tana k’ok’arin saukar da hakkinta na gaisuwa dana abinci, amma sam bayako kallon dinning table, kullum sai dai ya hada porridge yasha, gashi scent din abincin ta na shiga har hanjinsa don tsabar dadi, amma saboda fadin rai da miskilanci irin na Saifullah ko kallo mai abincin da abincin basu isheshi ba..

Haka dai ta koma makaranta, haduwar su kullum sai magrib, ta gaisheshi ya amsa a dak’ile, har bikin Lee ya ‘karaso, da ita aka karbi lefe da komai, aka fara shirin biki, su bridal tea party da duk sauran events da akai Islam taje, domin Ya Bala ya aiko mata da kyautar mota, tuni harta koya cikin sati biyu ta kware. Ita ta tuk’a kanta ko’ina, ita har addua take yi Allah ya kawo k’arshen wannan ‘kaddararren auren nata da Saifullah, tunda ta gano baya sonta ba kuma zai tab’a son taba a cewar ta, domin shekaran jia abunda yace mata kenan, ‘baya son ta ba kuma zai tab’a son ta ba’. Ta ajiye kalmomin sa a kundin zuciyar ta, sosai tai musu kyakkyawan mazauni.

Ranar lahadi aka kai Lee gidan ta dake nan garin Abujan, domin basu da nisa sosai ma da gidan Islam din, shiysa ma Islam ta ‘kara jin dadi, ganin ta samu y’ar uwa kusa da gidah. Monday da sassafe Islam ta gama gyaran ko’ina na gidan lungu da sak’o, ta sassaka turarukan wuta, riga da skirt tasa na English wears ta ‘dakko after dress shara-shara a hannu zata yafa, da babban mayafi wadatacce saboda yanayin zafin garin. A lokacin Saifullah ya sakko shima, sanye cikin Kaki na NYSC zai je monthly clearance, yana tafe yana taje sumar gashin sa, kallon kallo sukai ya dauke kansa, Islam ta daure ta dan rissina tana,

“Ina kwana?!”

“Lapia.” Ya fada a takaice yana wani shan kunu.

Ita dai Islam kitchen tayi abinta, ta had'a kayan breakfast dinta a wata y'ar jaka, ta zuge ruf abunta, a kitchen ta zura rigar ta yafa mayafin,bakin nan ya sha jambaki ja,Ta koma parlor inda yake, daga tsayen tace masa,

"Toh ni na tafi school, and I might be late today, Saboda yanayin lectures din namu na yau."

Tana gama fada ta juya zata tafi, Don kullum idan tayi masa sallama zata tafi baya tankawa, Ita dai tana k'ok'arin binsa ne kawai,

"Ke.." ya fada yana wani yatsina fuska,
Juyawa tayi tana kallon sa.Batare daya kalleta ba yace,

"Koma ki saka hijab, ki rage wannan lip stick din yan 'kauyen da kika sa, you luk so suffocating.."

Tabe baki tayi,cikin kasa da murya ta furta,

"Latsi.."

"Kika ce mene?"

"Da kai na nake.."

Ta bashi amsa da sauri tana komawa daki,gudun karta makara, kayan gaba d'aya ta canza, zuwa wani material blue and pink, ta zura jilbab tafito, Sam ta manta da maganar janbaki, zata wuce yai taku d'aya biyu ya riko ta,tuni jikin ta ya fara rawa, siririn tsaki ya saki yana harararta,cikin isa yace,

"Wato saboda ga sa'an ki ko? Na miki magana ki goge jambaki shine kikai ignoring ko?"

Shiru Islam tayi, tana raba idanuwan wannan bakon al'amari, k'ok'arin kwatar kanta take ya hana, ta hanyar riko hannayenta ya jasu can k'arshen corridor ya jingina ta,hannun sa sakale da kugunta, kafin tayi aune sai ji tayi ya had'a bakin sa da nata ya shiga yi mata wata irin sweet and passionate sumba mai ratsa jiki, mutumin ku daga shanye jambaki ba sai ya rike lips din yarinya ba, har wani lumshe idanuwa yakeyi, Ai kuwa da karfi Islam ta ture shi, yaita maza ya hade rai, ya yagi tissue yana goge kan bakin sa, zatai magana ya rigata cikeda borin kunya yace,

"Tun ba yau ba, nake kama ki kina satar kallon lips dina, sai gashi daga gwadawa kuwa kin rike mun lips sai kace kin samu alawa, idan nace ban yafe ..."

Katse shi tayi, tana masa kallon yaushe nai haka? ! Cikin bacin rai tace,

"Ni ce na rike maka lips?"

Ko kallon ta beyi ba ya fice daga wajen corridor yana nanata kalmar,

"So suffocating"

(THE START OF SOMETHING NEW; SAIFUL_ISLAM#LOVE STORY BEGINS🚴‍♀️)

_Unedited... Pls do ignore all typos😻_

_WRITTEN BY THE ELOQUENT WRITER:MISS XOXO🧕_
[1/3, 10:53 PM] Miss Xoxo: *_SAIFUL_ISLAM...💕*_

*_NA*_

_*©NANA HAFSAAT*_
*_(MISS XOXO)*_

_*®HASKE WRITERS ASSO.💡_*

*_SADAUKARWA GA:*_
_ASY KHALEEL💕_

*_TUKWICI NE GARE KU:*_
_YA HAJJAH CE😻_
_BILLYN ABDUL😘_

*_SHAFI NA 54-56_*

_nanahafsat.wordpress.com_

Saifullah na tsaye a bakin ‘kofa, yanata ayyana yadda zai sauke wa Islam kwandon rashin mutunci, na barin sa da tayi a tsaye tamkar ‘dan aike. Islam dake baje akan gado tana danna waya ta ajiye ta a gefe, jin knocking din da yake ya isheta, cikin turo baki gaba ta nufi hanyar ‘kofa domin bude masa, gaba d’aya ta ‘dauki darasin Lee a kanta, chewing gum ne a bakin ta, tana taunawa. Sanye take cikin wata shegiyar rigar bacci armless. Gaba d’aya santala-santalan cinyoyin ta sun bayyana a waje, domin rigar shara-Shara ce, ‘kirjin ta kuwa tamkar zai fito ta gaban rigar tsabar kamata da tayi.

A yangance ta bude ‘kofar tana yatsina fuska, Saifullah dake shirin zubo mata kwandon masifa, ya bude baki kenan zai yi ya kasa, ganinsa da jinsa sai suka tsaya cak akan siffar Islam. Bin ta yake da kallo, kamar ‘dan ‘kauye yazo birni. Yana ‘kissina abubuwa da yawa a zuciar sa. Tabe baki Islam tayi, ta wuce abunta tana juya mazaunanta, wani kakkauran yawu Saifullah ya hadiye, irin na kwadayin abun da kakeso aka hanaka ‘dinnan. Har ta koma daki bai dena kallon taba, tundaga saman ta zuwa ‘kafarta. Jiki ba ‘kwari Saifullah ya kullo ‘kofar. Dakyar ya hau sama yana hawa kowanne matattakalar bene yana bin dakin Islam da kallo. Ji yake wani abu na ingiza shi, kan yaje gareta amma ya kasa.

Islam kuwa tana komawa ‘daki, ta shiga bawa Lee yadda sukai ta WhatsApp. Take bacci ya ‘dauketa bayan ta yi alwala ta sauya wani kayan baccin, Don dama wannan tasa ne don tsokano Saifullah,  Saifullah dake sama kuwa ya nemi bacci a idanunsa ya rasa. Yayi sallolin nafilfili da addu’oi, amma sam bacci yak’i ‘daukar sa. Daya rufe idanu siffar Islam kawai yake gani, Wani sabon yanayi yaji yana shiga jikin sa, tunani sosai ya shiga yi, cikin haka kuwa bacci ‘barawo ya sace shi...

*WASHE-GARI*

Islam bata fito ba sai wajen 10, dake weekend ce, sanye tafi to cikin sequence lace blue, dinkin fitted gown, bata ‘daura ‘dankwali ba, tayi kalba guda biyu manya da suka zubo mata har gadon bayan ta. Tasha jambaki. Tana fitowa sukai kicibis da Saifullah dake zaune a kujera ya saita ‘kofar dakin da zata fito da kallo. Kallo d’aya zakai masa kasan bai samu bacci ishasshe ba. Ko kallon sa batai ba ta ‘dauke kanta, y’ar gaisuwar da yake tsammanin samu ma ranar batai masa ba. Kitchen tashi ga, cikin ‘kan’kanin lokaci ta soya chips and egg, ta kira mai gadi a waya ya karbi nasa. Kanta tsaye ta wuce ‘dakinta da nata plate din a hannu. Saifullah dake kan kujera ya zama kamar wani mutum-mutumi. Ganin ko takansa bata biba, yau ko tayin abinci batai masa ba. ‘Kwafa yai yana mikewa tsaye. Mukullin motar sa ya zira rai ‘bace ya nufi gidan su Khaled.

Lokacin kuma Humaira tagama bawa Haj Latifa labarin komai. Ita ma kuwa batai ‘kasa a gwiwa ba ta buga tafawa Haj Zuwairah. Haj Zuwairah kuwa lokacin sunata shirye-shryen dawowa Abuja a satin. Wayarta kare a kunnenta ta jiyo muryar Haj Zuwairah na ‘kark’are xancen da,

“Na baki wuk’a da nama auntyn su, ki dau duk matakin da kikaga ya dace, kafin mu dawo, Insha Allah ni nasan me zan yanke akan al’amarin..”

A lokacin kuma Haj Latifa sallama takewa Haj Zuwairah, Ai kuwa Saifullah ya shiga parlorn bakin sa ‘dauke da sallama. Haj Latifa tai murmushi kawai tana cewa da Haj Zuwairah ta cikin waya,

“Kin ganshi ma ‘dan halak yazo. Okay to shikenan, Duk dai yadda ake ciki zan sanar miki.”

Cewar Haj Latifa ta katse kiran bayan sunyi sallama, Saifullah ya zauna a gefan kujerar da Humaira take, mikewa Humaira tayi bayan ya zauna, fuskarta a had’e ta gaishe shi, Don sosai take jin haushin abubuwan da yake yiwa Islam, bai kawo komai ba ya amsa da,

“Lapia lou Humaira, ya studies?”

“Kalau..” kawai tace a takai ce, ta haura sama abinta.

Har ‘kasa ya tsugunna yana gayda Haj Latifa, fuska a sake ta amsa, sosa ‘keya ya shiga yi, hakan ya sanyata tambayar sa ko lapia? Ya amsa da,

“Lapia lou Aunty.. Porridge(abinci me ruwa-ruwa) nake so..”

“Toh bari na sa ayi maka kunu.. Ina ita Islam ‘din take, ko tana school?”

Sai duk kunya ta kama shi, ya zama guilty conscious, ya ma kasa magana, Hakan yasanya Haj Latifa kyautata zaton dagaske ne de maganar da Humaira ta fad’a mata. Murmushi kawai tayi. Bayan ta mike ne tace dashi,

“Bari a damo maka, a hada maka da cup cake?”

Daga kai yayi kawai alamun Eh, yana jin sa duk a takure. Fita Haj Latifa tayi, ta shiga kitchen da kanta ta hado masa kunun tsamiya da chocolate cup cake.

Islam kuwa bayan fitar sa, ta shiga study room, dake sama, cikin sauri ta debi books din da takeson dubawa ta koma kasa, Don tunda akai auren ita a dakin ‘kasa take, shi kuma yana sama. Dama sama ‘daki uku ne da parlor sai kitchen, ‘kasa kuma daki ‘daya ne da parlor biyu, sai dinning area da kitchen/ store, sai daki d’aya a waje da balcony.

A ranar ne da rana ahalin Prof. Khaleel suka yiwa Islam zuwan ba zata, Ai kuwa taji dad’in zuwan su, ta sake wata kwalliyar tana bude musu kofa, Ammi ce kawai bata zo ba, amman Yakolo ta wakilce ta, da abincin su suka zo, nan aka shiga ci ana shafta, Saifullah kuwa bayan ya bar gidan su Khaled majalisaar su ya tafi, har yaje zai yi parking yaji gangar jikin sa na ingiza shi da ya koma gidan sa, zuciar sa na kwad’aita shi da son ganin Islam, idanuwan sa na nuna masa kyakkyawan murmushin ta, da tastiest lips dinta masu rugurguza mai tunanin sa.

“So suffocating...”

Ya fada yana mai dukan sitiyarin motar sa, kan motar ya juya ya koma gida, tun a kwanar gidan sa ya hango motoci, lambar kano da na Abuja, mai gadi ya bude masa gate ya shiga ciki, tun daga gate yake jiyo hayaniyar su, anata zuba hira. Lado mai gadi ya kalla dake zuba masa kirari, cikin melodious muryar sa yace,

"Baki mukai ne Lado?"

"Eh oga.. 'yan uwan hajia ne suka zo d'axu."

Kad'a kai yayi, ya shiga cikin gidah da takunsa na 'kasaita, bakin sa 'dauke da sallama, idanuwan sa suka zumo masa Islam dake zaune a tsakiyar wasu mata sai hira take zubawa, mamaki yake na ganin dama tana hira haka? Kansa ya 'kara daurewa ganin Saifullahi da yayi, hankali kwance yana kurbar lemon robar hannun sa, Sai a lokacin suka lura da shi, aka shiga gaggaisa wa, shima cike da kunya yake amsa musu, ya bawa Saifullahi hannu suka gaysa, duk abunnan idanuwan sa na kan Islam dake dankaramai harara idan sun had'a ido, Sama ya hau , yana yi yana kallon Islam. Ganin haka yasanya Yakolo murmushi ta dubi Islam dake basu labarin makarantar su tace da ita,

"Islam je ki kai masa abincin ko? Ya dawo ko sannu da zuwa baki masa ba, shashasha na 'dauka da kikai auren kinyi hankali.."

Cikin zumburo baki gaba Islam ta mike, duk yan parlorn suka sa daria, a nata 'bangaren kuwa damuwa ce fal, na ganin su basusan halin da take ciki ba, ba susan irin zaman cakwakiyar da suke da Saifullah ba, harda bubbuga 'kafa tai a 'kasa irin na shagwabar nan, Yakolo ta kai mata dukan wasa, Ita dai Islam 'murmushin da yafi kuka ciwo kawai take musu tana yak'e, Don kar su gano kan abun. Tana hawa bene tana addua, gaba d'aya a tsora ce take batasan irin bakaken maganganun da zai sake gasa mata ba. Duk abun nan Saifullah na kwance akan gado, yana kallon su ta madedeciyar tv da aka hada domin dakko rahotan cctv dake parlorn da suke, da kuma sauran ko'ina na gidan, bai tab'a kunna taba sai yau, Don sosai zuciar sa take sake kwadai ta masa son ganin Islam. Yana ganin ta kusa 'karasowa dakin da yake yai maza ya kashe tibin (TV/television). Islam kuwa cikin sand'a ta shiga parlorn sama, daki d'aya ta bude tana adduar Allah yasa baya ciki. Ai kuwa ba kowa ciki, ta shiga tana sauke nannauyar ajiyar zucia.

Saifullah dake maitar son ganin ta yaji 'dif , ba Islam ba alamar ta, cikin rawar jiki ya mike yana gyara collar rigar sa, ya kara banka turaren alharamein yana kallon kan sa a mudubi. Cikin hanzari ya fita daga dakin, ta kamshin turaren ta ya gano tana dakin tsakiya. Ai kuwa yana murda handle din kofa ya hangota a zaune akan gado tana raba idanu, daria taso tabashi ya danne, yana wani hade rai tamkar yaga kashi, kamar bashi ne mai 'kulaficin son ganin ta ba. Tana ganin sa ta 'kara sunkuyar da kanta. 'Kasa 'kasa ya shiga kallon ta, ba kadan ba tayi mai kyau cikin wani material lallausa ja, dinkin bubu, tasha jan jambaki, dauri kawai tayi bata yafa mayafi ba, jelar kalba biyun da tai ta matukar karawa daurin kyau.

Kusa da ita ya matsa, ta ja baya da sauri, sai da suka kai ‘k’arshen gado a haka, ya samu kansa da rike hannun ta, Cikin murya ‘kasa kasa kamar rad’a yace da ita,

“Who’s that guy?!”

“Wa kenan?” Ta bashi amsa tana cuno baki gaba, amma fa a tsorace take.

Hade rai yayi kafin yace,

“Na downstairs mana.. Wanene shi?”

“Oh ya Saifu... Cousin dina ne”

Kamar almara yaji abunda ya tsaya masa kwana da kwana ki a wuya yau ya sauka ‘kasa ya fad’a.

“Cousin?” Ya maimata yana feeling guilty.

Daga kai tayi tana kallon gefe, samun kansa yayi da ‘kara tambayar ta da,

“Malamin ku ne a school ko kuma student ne shima?”

Wani kallo ta watsa mai kafin tace,

“Malamin mu ne, shine lecturer dinmu na community medicine.”

Idanuwan sa ne suka sauka a kan labbanta, wani feelings yake ji a game da su na daban, So yake ya samu ya rage xafi akan su miskilancin sa ya hana, dakyar ya ‘ka’karo maganar,

“Wane warning na miki akan jambaki?”

Ta gano shi, hakan yasanya ta saurin kwace kanta ta mike a dari zata buda kofa ya rigata, ita da kofar ya had’a ya rufe da mukulli, ya jinginata a jikin kofar, yana kallon idanuwanta dake sanye cikin kwalli baki me kyau. Cikin takaici tace,

“Dan Allah ka sake ni na koma wajen su Aunty.,, Dan Allah ka..”

"Ya Fati!.."

"Na'am Islam, Kiyi kwanciyar ki, magana nake so muyi da ke ta fahimta, kuma inaso ki 'dauke ni tamkar da Safah ko Marwa kike magana, shawarwari zan baki, wanda idan dai kikai riko dasu Insha Allahu rabbi zaki samu riba sosai agidan mijin ki.."

Cikin 'kasa da kai Islam tace,

"Tohm Ya Fati! In sha Allah...."

___________

_Ya labarin Karime? Tana can rai a hannun Allah, rashin lapia kullum 'karuwa take yi, sai dai adduar Allah ya yafe mata kawai, ta nemi gafarar su Haj Aysa, kuma sun yafe. Domin har dubo ta sai da suka niki gari har Kano suka dubo Karime, wadda ta dulmiya a kogin ciwon mutuwar jiki(paralyses), hepatitis (ciwon hanta) da kuma ciwon kansar mama, (breast cancer)., Yan uwa dayawa sun guje ta, domin lokacin da take cikin SAMU, bata dama wa dasu, Su kuma yanzu suke ramawa tunda tana cikin RASHI...._

_Yafendo kuwa tusa sai gaba take yi, sannan kullum sai aljanu sun firgitata, da alama turen da tai a baya ne suke bibiyar ta, da temakon Allah dai ta warke da 'kyar, amma ta kamu da ciwon 'kafafu mai tsanani, wanda ta kai ga tadena tafiya, da alama dai mutuniyar taku ababe marassa kyau data taya Karimatu suka shuka, shi take girba, har waje an fitar da ita, anyi gwaje-gwajen su MRI, X-RAY, SCAN amma duk komai normal ne, daga 'k'arshe sai rugar Baffa Ardo, Prof Khaleel ya mai da ta, kan idan ta warke sai a 'dakko ta.. ga tusa ga ba iya tafiya, data saki 'daya ake darewa, Saboda tsabar wari, amma ta 'dau hakan ta ajiye a matsayin alhakin su Haj Aysa ne yasa ta koma haka, ta kuma godewa Allah da sakayyar da ta samu kad'an ce, tafiya dai tadena yin ta har abadah, Sai dai fatan Allah ya kawo sauki._

_Hmm Bangaren Hilaal kuwa rashin virginity din Hibba yana damun sa, domin ya gano y'ar iska ce kawai aganin sa, Saboda daya tursasata ta fad'i gaskia ca tai shima taji labarin haka yayiwa mata biyu a Nigeria har su biyu, kuma 'yan gidah d'aya. Ya mike zai daketa ta dire tsallen albarkar wallahi bai isa ba, yana dukanta zata rama, kuma ta kai 'kararsa wajen iyayen sa, kuma aure da sukai na zobe ne, babu yaji bare SAKI. Kyaleta kawai yayi amma duniya ta chake masa, gaba d'aya kwakwalwar sa ta zama malfunction.ya fadawa wani malami yadda ake ciki, bai boye masa komai ba. So sai malamin yaja hankalin sa, ya 'kar'kare masa da cewar,_

_*YANA DAGA CIKIN ILLOLIN DA ZINA TAKE HAIFARWA TUN ANAN DUNIYA...._*

_1-RUSHEWAR TATTALIN ARZIKI: annabi (saw)ya bayyana acikin hadisi cewa dukkan, society da suka ta'allaQa da aikata al-fasha. Allah madaukaki yana dankwafar dasu ta fuskar tattalin

arziki dss,_

_2-GUSHEWAR KUNYA: annabi (saw) yace da imani da kunya dan-juma ne da dan-jummai, muddin 1 ya tafe to 1n ma baya zama,_

_3-YA‘DUWAR ANNOBA / CUTUTTKA: annabi,(SAW) yace zina bazata bayyana ba kowa, yana aikatawa ba shuwagabanni da, mabiya face sai Allah me girma da daukaka ya saukar wada mutane annoba / cututtuka, Dan-uwa ka dubi yanda HIV/ AIDS yake kashe mutanenmu, Allah ya kyauta,_

_4MUDDIN KAYI SAI WANI YAYIWA NAKA: annabi (SAW) yace ita zina BASHI ce, inkayi sai an maka, Duk wanda yayi zina da “yar-wani ko uwar-wani ko yayar-wani, to shakka babu sai anyi da nashi akwana atashi, Allah sarki hakan ya faru a yankin mu, Wani mutum ya kasance me tsanani wa yarsa (mace) kasancewar ta girma ya hanata fita koda makaranta ne, kullun haka---Rannan saiga “ya“ da ciki, Karshe yasa mata wuk’a awuya kota fa‘da, wanda yayi mata ko ya yanka ta, Qarshe tace - ina wannan Qawarta me zuwa yau-da kullum akace ‘ei‘ tace ba mace bace, namiji ne, Kaga illan zina kenan, yana tunanin ya tsira, sai gashi har gidah anzo anyi wa ‘y’ar sa._

_5-GUSHEWAR MUTUNCI/KIMA ACIKIN JAMA‘A:,ka kula duk wanda yake zina to Allah saiya, cire masa kima da kwarjini acikin jama‘a, zaka ga bashi da kima acikin mutane._

_6-MUTUWA BA IMANI: annabi yace duk me, aikata zina al- fasha o Allah ze zare imani, daga gareshi Qarshe ya mutu ba imani_

_”Annabi yace duk wanda yayi zina da matan, aure- to Allah ze kwashe dukkan aiyukan sa, na al-khairi yabawa mijinta, Aranar tashin al-Qiyama kuma Allah ze masa, azabar rabin wannan al-ummah ita matar ma haka. Innalillahi wa‘inna ilaihir-raju‘un !!_
_Annabi yace babu laifi da Allah yafi kyama, sama da mutum ya saka;_

_AL-AURANSHI A CKIN FARJIN HARAM !!_

_”Dan-uwa na ka sani aduniya dayan shirka wa Allah da kisan kai babu laifi dayafi girma sama da zina !! Allah ka mana katangar Qarfe da aikata zina_”

_Take hawaye suka fara reto daga idanuwan Hilaal, tuni zuciar sa ta yarje masa ya koma Nigeria ya nemi gafarar Hidaya da Hafsaat...._

<><><><><><>>>

XAFAFA BIYAR;

DAURIN BOYE; NA HUGUMA

BURI DAYA; NA MAMU GEE
SAUYIN KADDARA NA;HAFSAT RANO
WUTSIYAR RAKUMI; BILLYN ABDUL
KAI MIN HALACCI NA MISS XOX

ga mai buqatar littafan zafafa biyar dukansu ko wasu daga ciki sai ya biya 500 ga dukka litattafan,ko 200 ga littafi daya,ko 300 ga littafi biyu,ko 350 ga liitafi uku,ko 450 ga littafi hudu*

*za'a tura kudin ta wannan accnt number din*

Hafsat kabir umar
0225878823
GT bank

Saika tura shaidar biya ga wannan number

08030811300

Ga masu turo da katin waya kuma zaku tura katin MTN ta wannan number din

07067124863

Da zarar kin biya kai tsaye zaki tsinci kanki cikin gidan da zaki samu littafin da kika biya.

*Karki bari ayi babu ke*🤝🏽🤝🏽🤝🏽

DAURIN BOYE; NA HUGUMA
BURI DAYA; NA MAMU GEE
SAUYIN KADDARA NA;HAFSAT RANO
WUTSIYAR RAKUMI; BILLYN ABDUL
KAI MIN HALACCI NA MISS XOXO

_WRITTEN BY THE ELOQUENT WRITER:MISS XOXO🧕🏽_
[1/3, 10:54 PM] Miss Xoxo: *_SAIFUL_ISLAM...💕*_

*_NA*_

_*©NANA HAFSAAT*_
*_(MISS XOXO)*_

_*®HASKE WRITERS ASSO.💡_*

*_SADAUKARWA GA:*_
_ASY KHALEEL💕_

*_TUKWICI NE GARE KU:*_
_YA HAJJAH CE😻_
_BILLYN ABDUL😘_

*_SHAFI NA 68_*

_SHAFIN YAU NA KI NE *LIEEMERH😍*💕, FATAN ALKHAIRI A GARE KI, NAGODE DA YADDA KIKE BIBIYAR LITTATTAFAI NA, JAZAKILLAHU BIL JANNAH🤲🏻💙_

_nanahafsat.wordpress.com_

*Dr* Jalaludden ne ya shiga ‘dakin da Saifullah yake jinya shi da su Mami da Fatima, daga baya kuma su Aji Mommodu ne da Alhaji Faruk, Islam na ganin su taja baya tana sunkuyar da kanta a ‘kasa. Saifullah kuma yak’i ‘dauke idanun sa daga kallon ta, kan sa su kayi suna tambayar sa ya jikin na sa? A hankali yake basu amsa, dr Jalaludden yai ‘yan rubuce-rubucen sa a file ‘din Saifullah dake hannun sa, kafin ya dora hannun sa akan goshin Saifullah yana cewa,

“Ya kake ji yanzu?”

“Kai na ne yake ciwo sosai, sai zucia ta, tana mun zafi”

Saifullah ya ‘karasa fada yana ‘dan cizan leban sa alamun zafin ciwo, Dr ya kad’a kai kafin ya sake cewa,

“It shall be well Insha Allah, duk zasu dena..”

Ya sake mai da kansa gurin su Aji Mommodu kafin yace,

“Zamu ‘dora shi akan magunguna na kwana uku, da ‘karin ruwa saboda yaji ‘karfin jikin sa, yanzu dai a kawo masa abu me ‘dan ruwa-ruwa, sai kuma a bar mutum daya ya taya shi kwana

ki ukun sa, sauran kuma su koma gidah, Saboda yana bukatar hutu, banda hayaniya...”

Yana gama fad’a ya fice, bayan ya musu sallama, duk maganar da ake da Saifullah idanuwan sa na kan Islam, duk tabi ta rud’e da yadda ya rufe ta da mayataccen kallo. Cikin haka Abbas ya shiga shi da su Aunty Lateefa, hannuwan su rike da food flasks na abinci, da sauran abunda za’a bukata..
Bayan sun gaggaisa ne Aji Mommodu da Alhaji Faruk suka fita, kan za su dawo anjima.

Haj Zuwairah ta zuba wa Saifullah kunu a cup, Abbas ya taya shi ya zauna, yana sipping kunun a hankali, sai daya shanye tas, Mami ta mike tana cewa da Abbas,

“Abbas ka zauna a wajen Saifullah pls, har a sallame shi. Kwana uku ne kawai, da safe mu sai mu dinga zuwa kai kuma ka tafi gidah, adai dinga shifting, sa..,”

Bata ‘karasa ba Saifullah ya ‘bata fuska yana cewa,

“First love ni dai abar Islam pls, wane Abbas kuma, ni dai-ni dai kawai Islam ta...”

Mami ta dankara masa harara tana masa dak’uwa kafin tace,

“Saboda me za’a bar Islam? Shin zata iya daukan kane ta kai ka bandaki ko kuwa zata juri daga ka ka zauna? Toh bazata zauna ba kaji na gaya maka, Abbas dai naka shi zai zauna ya taya ka jinyar, danma an temaka ma, da ni bashiru mai gadi zan sa yataya ka kwanan ma sai kuma ga Abbas nan yazo.”

Abbas dake gefe ya shiga daria yana rufe baki, idan sun had’a idanu da Saifullah kuma ya masa gwalo, Saifullah ya shiga kumbure-kumburen fuska yana kunkuni shi kadai, sallama su kai masa suka fara fita, Haj Zuwairah ta dubi Islam kafin tace da ita,

“Auta ta! Ko zaki kwana anan din?”

Islam tai saurin girgiza kai, alamar a’a, Hajia Zuwairah ta sake cewa,

“Toh kuyi sallama, zamu jira ki a waje.”

Kamar bango ya tsage ta fada, haka Islam taji, Abbas ya fice shima, daki ya zama saura su biyu, mika mata hannuwa yayi kafin yace,

“Come to me love...”

‘Karasawa tayi tana tab’e baki, saurin kamo hannun ta yayi yana matsawa, ciki-ciki yace,

“Meyasa kika ce da first love ba zaki kwana anan ba?”

"Saboda ba na so"

Murmushi yayi kafin yace,

"Okay fine! Yanxu dai me zan samu na goodnight?"

Ware idanuwa Islam tayi, cikin turo baki ta..... taji ya hade bakin su, silent Greece kisses ya shiga bata, hawaye ya fara zuba daga idanun sa, Islam taji danshi a fuskar ta, ta shiga kiciniyar 'kwace kanta ya hana, Saifullah ya zare bakin sa daga nata ahankali ya sa hannun sa yana shafa kanta zuwa bayanta, a kunnen ta ya shiga rad'a mata,

"You make me fall in love darling... I love you, I love you, Dan Allah kakki guje ni, duk rintsi kakki bari a raba auren mu, wallahi wallahi ina son ki Islam, Meyasa bakya so na? Idan akan lefin da nai miki a baya ne, I'm ready to sacrifice my everything just to make you happy, me zanyi ki yafemin?! Kinji.. Islam... uhm? Talk to me.. I'm going gaga.. Love. ki mun magana pls"

Yafad'a yana hura mata a iska a kunne, harshen sa ya zura yana licking kunne, cikin zuciar ta tace

"Mutumin nan dan iska ne tab"

Dakyar ta 'kwace kan ta, tana gyara mayafin ta, sai da takai k'ofa sannan ta juya tace dashi,

"Get well soon.."

Ta fice cikin sauri, nan ta samu su Haj Zuwairah na jiran ta, cikeda kunya ta shiga motar suka fice, shi kuma Abbas ya koma 'dakin, ya tasa Saifullah a gaba yana masa daria, sai da yai mai isar sa kafin cikin gwada muryar Saifullah yace,

"First love da ma Islam aka bari.."

Ya shiga daria harda rike ciki, Saifullah ya zabga mai harara yana juya mai baya kafin yace,

"Ai ni an cuce ni wallahi, da za'a rasa wanda za'a had'a ni da shi sai kai, 'katon banza da kai, gwauro marar mata...Mts"

"Eh ana dai had'a, kuma dole da katon banzan zaku kwana a 'daki d'aya, jarababbe bakada lapiar ma sai ka 'kwakwume yarinyar mutane, banza marar ta ido( kunya).."

"Eh naji, ai halaliya ta ce, matata ce ai, So suffocating."

Tsaki Abbas yayi, kafin ya shjga daria sai da yai mai isar sa kafin yace,

“Kai baccin ka kawai, angon Islam, autan Mami ‘dan gidan Uncle Modu bada kanka asare..”

Haka dai Abbas ya shiga tsokanar Saifullah suka raba dare suna abu d’aya... Cikin kwanaki ukun nan Saifullah a daddafe yayi su, domin ko sau d’aya Islam bata sake zuwa ba saboda hot practicals suke yi, kuma mostly night lectures ake musu,

A ranar da za’a sallamo Saifullah ne Aji Mommodu ya kira Islam ya tambayeta zata zauna da Saifullah ko ya sawwake mata? Ya ‘kar’kare da,

“Kar kiji komai Islam, idan har bakyason Saifullah kar ki cu ci kan ki, idan kuma ki na son ki koma ‘dakin ki to, duk dai zab’i ya rage na ki...”

Kanta a ‘kasa tana wasa da jelar hannun rigar ta tace,

“Zan koma ‘daki na Baba...”

Haj Zuwairah da Fatima da ke labe suna sauraron su, jin abunda Islam tafada yasa su sakin lallausan murmushi......

——-

XAFAFA BIYAR;

DAURIN BOYE; NA HUGUMA
BURI DAYA; NA MAMU GEE
SAUYIN KADDARA NA;HAFSAT RANO
WUTSIYAR RAKUMI; BILLYN ABDUL
KAI MIN HALACCI NA MISS XOX

ga mai buqatar littafan zafafa biyar dukansu ko wasu daga ciki sai ya biya 500 ga dukka litattafan,ko 200 ga littafi  daya,ko 300 ga littafi biyu,ko 350 ga liitafi uku,ko 450 ga littafi hudu*

*za'a tura kudin ta wannan accnt number din*

Hafsat kabir umar
0225878823
GT bank

Saika tura shaidar biya ga wannan number

08030811300

Ga masu turo da katin waya kuma zaku tura katin MTN  ta wannan number din

07067124863

Da zarar kin biya kai tsaye zaki tsinci kanki cikin gidan da zaki samu littafin da kika biya.

*Karki bari ayi babu ke*🤝🏽🤝🏽🤝🏽

DAURIN BOYE; NA HUGUMA
BURI DAYA; NA MAMU GEE
SAUYIN KADDARA NA;HAFSAT RANO
WUTSIYAR RAKUMI; BILLYN ABDUL
KAI MIN HALACCI NA MISS XOXO

_WRITTEN BY THE ELOQUENT WRITER:MISS XOXO🧕🏼_

[1/3, 10:54 PM] Miss Xoxo: *_SAIFUL_ISLAM...💕*_

*_NA*_

_*©NANA HAFSAAT*_
*_(MISS XOXO)*_

_*®HASKE WRITERS ASSO.💡_*

*_SADAUKARWA GA:*_
_ASY KHALEEL💕_

*_TUKWICI NE GARE KU:*_
_YA HAJJAH CE😻_
_BILLYN ABDUL😘_

*_SHAFI NA 70_*
_*EPISODE FINALE (KARSHE)_*

_nanahafsat.wordpress.com_

“Toh..Zan danja hankalinki akan yadda ya kamata ki dinga tarairayar Auta ta siga daban-daban kamar;  kissa, jan hankali da kuma ladabi da biyayya kowanne xan daukeshi d’aya bayan d’aya namiki bayani akansa, Kisani dukkan xamantakewar rayuwar aure ba xata yiwu ba saida kissa, idan akace miki kissa ta kunshi abubuwa da yawa, kissa ta kasu kashi biyu akwai kissa marar kyau akwai kuma kissa me kyau, Mara kyau itace ta shirye tuggu da makirci da sihiri, Za ki ga kishiya ta kullawa kishiyarta sharri ko idan ta daidaici ta gama girki taje ta tsuga mata gishiri ko yaji ko kananzir ko kuma tai k’ok’arin fitar da ita daga gidan ma gaba d’aya, zaki ga mace ta shiga tsakanin d’an mijinta da mijin,

“Ta cikin dabara ko mace tashiga tsakanin mijinta da iyayensa da makamantansu wannan kissa mara kyau sede muce tur da ita. Allah ka ganar da masu irin wannan kissa, Amma kissa mai kyau itace kulawa da mai gidah da tarairayarsa kamar kwai wanda daga ciki akwai, Kissar magana, kissar tafiya, kissar kwalliya, kissar abinci, kissar tsafta, kissar kallo mind you ba kallon film ba to kallon miji nake nupi, yawwa se kissar shagwaba da kissar kwanciya se kissar kula da jikin mai gidah suma xan d’auki kowanne nai miki bayani akansa Ina fatan kina ganewa?!,

Cikin k’asa da kai Islam tace,
“Eh ya Fati..”

“Kissar magana: idan xakiyi magana da mijinki ki kasance cikin nutsuwa da tauna magana da xaki gaya masa kafin ki fadeta don gudun gaya masa maganar da baxai ji dadinta ba ko bata masa rai, Ki dinga magana cikin sigar hankali karki dinga bud’e masa muryarki kala kala wani lokacin ki maketa wani lokacin ki dan budeta wani lokacin ki dinga yi a hankali kamar bakyason magana, wataran kuma idan kinason gaya masa magana mai dadi ko ta soyayya kice saiya baki kunnensa xaki rada masa. Sai kissar mu ta gaba,

“Kissar tafiya; idan xakiyi tafiya kuma kin tabbatar yana gurin ko yana kallonki daga inda yake ki dinga tafiyar da xata dauke masa hankalinki xuwa gareki misali ki dinga tafiya a hankali kamar bakyason taka k’asa wani lokacin ki dinga tafiya kina karairaya kina dan jujjuya jikinki wani lokacin kuma sauri sauri xaki dingayi kina juya maxaunanki idan ta gaba yake kallon ki kisan yadda xaki dan dinga girgiza kirjinki cikin hikima bata sigar da xai gane ba, amma fa Islam mijinki kad’ai xaki dinga yiwa wannan kala kalar tafiyar cux kikaiwa wani xaki dau zunubi ne,”

Cigaba da koyamata kissoshi tadingayi kama daga kissar kwalliya, da kissar abinci kissar tsafta, da kuma kissar kallo ciki harda kissar shagwaba data kwanciya, wanda sosai Ya Fati taja kunnen Islam akan kissar kwanciya ta kar kare mata da yadda xatai kissar kula da jikin mai gidah,

"Hope kingane?!"

"Nagane Ya Fati" cewar Islam datai wiki-wiki da idanuwa wai yau Ya Fati ce take hira da ita, hirar ma ta manya duk kunya ta davaibayetaa

"Yawwa to sai dan karin jan hankali daxan miki wanda idan kika dumfafi yinsa tabbas xaki xamo shalele awurin mijinki yaxamto ba wacce yakeso da gani sai ke hanyoyin jan hankalin sune,

"Kula da duk wani abu da mijinki yafi so,ki kula sosai da duk wani abun da bayaso ki lura da abinda yake damunsa da hanyar da xaki kula da iyayensa da danginsa da yadda xaki xauna lafiya da kowa babu ruwanki da wani kishi na banxa da wofi wanda xe kaiki ga hypertension, kishi dole ne ba ace karki ba amma akwai irin kishin da akeyi bana yanxu da yaxama na hauka ba, kede babu ruwanki don baki taso kinga anayi a gidan ku ba...

Islam ta daga kai, tana tuno irin buga kishin da ake a gidan su, Fatima ta ci gaba da cewa,

"Na ga, ga Ammi nan da Maman Arfat  kamar ya da kanwa haka suke abun sha'awa ba'a taba jin kansu ba ina fatan kina ganewa?!"

Kad'a kai Islam tai tana wasa da yatsun hannunta cikeda nutsuwa. Ya Fati  ta cigaba da yi wa Islam jan hankali akan rayuwar gidan miji ta k'ark'are da,

"Abu na k'arshe shine ladabi da biyayya, babbar magana kenan domin duk abubuwan dana fada abaya idan ba ladabi da biyayya yaxama na banxa don duk iya tafiyar ki ko iya farinki idan bakya yiwa miji biyayya meye amfaninsa?! Misali kinyi kwalliyar jan hankali kinyi masa kalar girkin dayake so jira kike ya dawo yaga kwalliya, Yaci abincin da kika tanadar masa amma yashigo ba sannu da xuwa ba karbar kayan hannunsa saidai ki bishi ki dire masa abincin da kika yi masa tana iya yiwuwa ma alokacin ki fara masa k'arar ko kudi da makamantansu toh tell me tayaya zaiga kyan kwalliyar sannan kuma yaji dadin abincin?!,

"Ko kiga wasu matan miji na magana suna yi suna fada sosai fad'i in fada bai dace ba sam kamata yai idan mai gidah yana fadansa kiyi masa shiru idan yagama sai ki bashi hak'uri idan kuma ke aka batawa baxaki iya bada hak'urin ba tunda ranki yakai kololuwa a baci to kiyi shiru kawai kuma ko menene yace kiyi masa koda kuwa ran naki a bace yake don kansa shima xe sakko ku shrya, Wasu kuma matan xaki ga suna yawan korafi akan maxajen su don abinda ba abin fada ba sai su rufe su da fada wasu ma kawai xakiga sun fice daga harkar matan kwata kwata inkinga sun kusancesu to sede idan rabo ya tsinke yawanci kuma xakiga akan maganar da mukai d'axu ne akan rashin gamsuwa damu da maxajen mu ba sayi xakiga mace har mace, Kamar ita tai kanta don kyau sai kiga sun had'a kishi da wadda bata kaitan ba harma xata xamto itace mai fada aji gurin mijin xakiga yana Allah Allah girki ya xagayo kanta don yafi gamsuwa da ita xakiga wasu matan suna yawan tambaya to meyasa wata macen ake gamsuwa da ita wata ba'ayi?!,

“Ba komai bane yake kawo haka kisani sai kowa da irin ni’imar da Allah yai masa misali kowanne jinsin halitta akwai maza akwai mata kuma both ana samun farare da bak’ake dogaye da gajeru mai kib’a da siriri ke kowanne abu dake jinsin bil adama xaki ga nawani yafi nawani to haka ma ni’ima take ajikin mata da maxan wata macen tanada ni’ima sosai bata buk’atar kari wata kuma tsaka tsaki ce wata ma bata da ita se d’an abunda ba’a rasa ba,

“Don haka Islam kisani kamar masu bukatar  karin jini da ake cewa ga abubuwan daya kamata suci haka ma matan masu neman k’arin ni’ima ajikin su akwai abinda yakamata suci domin ance idan kanada kyau to kadad’a da wanka,sai dai wasu matan suna amfani da magunguna barkatai wanda wasu ma basusan komeye ba sudai suci susha buk’atar su ta biya kawai shikenan, Wanda xakiga yin hakan xakiga yana haifar da cututtuka barkatai ga mata,shawara ta dake Islam karki xamto cikin irin wa’innan matan masu bankawa cikinsu kowane magani suka ji ance yanayi aa sam karki soma kowaye yakawo ko yaxo maki dashi karki soma amfani dashi kinji de na gargadeki domin hakan yana haifar da toshewar mahaifa,hana haihuwa ko canxawa yaro kamanni kamar wata k’awata sumayya matar ma’aruf wallahi abinda yafaru da ita kenan,Tahaifo yaro marar cikar halitta abun tausayi saboda ita komai cusawa take ta bankashi a baki duk bamu sani ba se bayan da xata haihu a asibiti dr tace har cancer magungunan suke sawa dakyar aka mata cs don kasa haihuwan tayi abu nabiyu ga kaikayin gaba wato infection,Da kurajen gaba plus ciwon ciki ke da abubuwa da dama de kede ki lazimci shan fruits kamar yadda kikaga ana saki sha anan su,

“Kankana,gwanda,ayaba,guava,lemo,tumatir,rake,aya,kwakwa,dafaffiyar gyada xuma,nono,madara,madaran shanu gurji cukwi,zogale da ruman da inibi se tuffa da kuma xaitun kina ganewa kuwa?!”

Nodding kanta kawai Islam tai gaba d’aya jikinta yayi sanyi se yanzu tasan tabbas aure aka mata batare da ya fati tadamu da damuwar da Meenah tashiga ba tacigaba da maganar ta,

“Se abu na k’arshe naga lokaci na ja, Auta yana ji ranki a kasa,Addua wato kirik’e addua, wallahi Islam addua makarin mumini ce ke duk wanda ya lazimci addua wallahi baxe taba tabewa ba azkhr dinnan kidinga yawaita yinsu nataho maki ma da wasu littafin du’as din suma ki rik’esu gidanki kullum yaxamto cikin karatun qur’ani musanman suratul baqra domin duk gidan da ba’ayinta ance kamar kango yake, Ki yawaita yin addu’oi na neman tsari ga korar shaid’an ya kuntata masu ya karyasu ke dama mutane ma sharranta masu nufarku da sharri, addu’a tana jawo yardar allah ta’ala, suna gusar da bakin ciki da bacin rai a zuciya,suna janyowa zuciya farin ciki da nishadi,suna karfafa zuciya da jiki,suna jawo arziki suna kara imani da tawakkul da sabr ke sunasa komai na mutum ya daidata ya samu peace of mind ki kama Allah Islam, kirike addua da qur’ani Insha Allah rabbi xaki bani labari,anan xan tsaya seki fad’i tambayoyin ki karkiji kunya ta Islam, ko tsoro saki jikinki ki fad’amun abinda baki gane ba.,

Shiru Islam tai tana k’as k’as da yatsun hannunta kunya dukta isheta jin shirun yayi yawa ne yasa ya fati sake tambayrta,

“Uhum Islam ina jinki”

“Ba..Babu komai ya fati duk nagode JazakillAhu khairan”

“Ameen..To shikenan dukde abunda baki gane ba ko kikeda karin bayani akai seki kirani awaya yawwa nasanki dama ke sarkin kamshi ce amma ki kara xage damtse khumras dinnan na wanka dana wanki da jiki dana moping duk fa kidage wajen amfani dasu kingade yadda mijin ki ke son kamshi, ki sake kaimi da sauran turarukhan jiki dana tsugunno dana kaya dana gidah du kulaccams dinnan duka kiyi amfani dasu, Idan sun kare kiyi waya ayo miki wasu koki had’a da kanki irin kamshin da kikeso aikin iya ko?!”

“Eh ya fati”

“To shikenan Allah ya miki albarka ki shirya, ga kaya nan da laffaya inji Mami, wannan kuma tsumin chad ne ki sha yanzu, karki mike sai bayan minti goma, wannan kuma cinye shi zaki tas, idan kin gama sai ki sakko, Allah ya sa ki koma a sa’a ya kad’e fitnah, ya baku zuri’a dhayyi ba...”

Cewar Ya Fati.. Ta karasa fada tana mai nuna mata komai da amfanin sa, a kunya ce Islam tace,

“Nagode Ya Fati, Allah ya saka muku da alkhairi, ya sa ki sauka lapia, Ameen.”

“Ameeen”

Cewar Fatima, ita kuma Islam ta mik’e ta shiga shirya wa...Hankali kwance ta gama kintsawa, tayi amfani da duk abun da Ya Fati ta bata tayi, admiring kanta ta tsaya yi ta cikin mudubi, ba kadan ba kayan sun mata kyau, lace din pink ne laffayar kuma pusher pink. Ganin su kadai ne ba kowa, yasa ta shafa pink jambaki, Ai kuwa ya mata kyau sosai, dan karamin bakin ta ya kama sosai da jambakin, abun dai sai fadar; soo masha Allah. Kasa ta sauka tun daga nesa Saifullah ya tsurawa Islam kallo, tamkar yau ya taba ganin ta, Haj Zuwairah da sauri ta ‘karasa ta rik’o Islam, Islam kuwa ta ‘barke da kuka, Don ba kadan ba takeson Haj Zuwairah, ganin ta ‘dauke ta kamar ‘yar data haifa, tare suka dinga kukan, domin Fatima ma sai da tai hawaye, sun bata tausayi, kuma ta lura mahaifiyar tasu na yiwa Islam din wani irin so tamkar ba sirikar ta ba.. Daga k’arshe dai Haj Zuwairah daki kawai ta shige ta rufe, Saifullah ya kama hannun Islam suka tafi, dai-dai bakin kofa ta cije tana shesshekar kuka, Ai kuwa yai mata ‘daukar jarirai ya direta a mota itada kayan ta...

A hanya ya tsaya ya sai kaji da kayan ‘kwalam da makulashe, suka nufi gidah yana aikin bawa Islam hak’uri, ba abunda yake kara tunzura kukanta irin first night din da Lee ta tsoratar da ita, Suna komawa gidah tai hanyar dakin ta, komai a killace a tsaftace, da alama Saifullah yasa an gyare gidan. Wanka ta sake yi ta feshe jikin ta da turarukha, nan Saifullah ya shiga shima da

kayan baccin sa, dauke da plate cike da kaji da sauran mouthwatering kayan dadi, a hankali yace mata,

"Love ga abinci sakko ki ci pls.."

Bin kazar tai da kallo ta 'dauke idanun ta daga gare sa, durku sawa yai kafafuwan sa zube a kasa yayi kneeling down, hawaye fal idanun sa, tuni suka fara wanke kyakkyawar fuskar sa, kafin yace.

"Dan Allah love kiyi hak'uri, ki yafemin, hakika nayi kuskure a da, amma inaso ki dau hakan ki ajiye a matsayin past life, love ko Allah da ya haliccemu muna masa laifi kuma mu roke shi ya yafe mana, so pls ki yafemin Love, kwatankwacin haka ma bazan sake miki ba insha Allahu, wallahi wallahi ni ba ma SO na ke miki ba 'KAUNAr ki nake, domin 'kauna bata karewa kullum daduwa take yi, So kuma yana raguwa kuma wani lokacin har dena yin sa ake yi, Ina miki son so, Ina miki son kauna, Ina miki tacacciyar 'kauna marar gauraye..."

Shiru yai yana goge hawayen fuskar sa, ahankali Islam tasa hannu ta 'dago shi tana goge masa hawayen kafin tace,

"Ni ma Ina kaunar ka Zawj, I love you pass my mind beyond my soul, ni ban rike kaba dama a raina, Allah ya yafe mu baki d'aya..."

Dadi Saifullah yaji, ya kama hannun Islam suka zauna, Kazar ya dakko ya sa mata a baki yana cewa,

"Ki ci sosai Love, wannan itace kazar amarcin mu, ki dau yau tamkar itace ranar da aka kawo ki gidan ki, kuma a yau ne zan shayar da ke zumar da tafi kowacce zaki, Ina fatan zaki bani hadin kai?"

Islam tai gum da bakin ta, Saboda ta gano nufin sa, Ai kuwa ya saki murmushi yana cewa,

"Matsoraciya..."

"Eh dai..."

Caraf ya hade bakin su, dama tun dazu yake muradin haka, sun jima suna abu d'aya, kafin su cinye kajin tas su ka kora da yoghurt, bandaki suka shiga atare sukayo alwala da brush, bayan sun kurkure da mouthwash na mint, Su kai sallar isha'i, sun 'dan tab'a kallo kafin su koma dakin sama, Saifullah yace da ita,

"Love tashi muyi sallar nafila mu godewa Allah, abisa azurtamu da yayi na samun junan mu.."

Daga kai kawai Islam tayi, suka yi sallar, Saifullah yaja ya zauna a gabanta yana mata

tambayoyi akan addinin musulunci, ta amsa dai-dai gwargwadon sanin ta, gado suka haye gaban Islam sai fad’uwa yake yi, Saifullah na hankalce da ita, janyo ta yayi jikin sa yana karanto adduar bacci;

“: اَللَّهُـمَّ بِاسْمِكَ أَمُوتُ وَأَحْيَا,”

Can kuma ya ‘kara da adduar saduwa da iyali(du’a when having relation with wife):

“: بِسْمِ اللَّهِ ، اَللَّهُـمَّ جَنِّبْنَا الشَّيْطَانَ ، وَجَنِّبِ الشَّيْطَانَ مَا رَزَقْتَنَا”

Benefit;
Ibn Abbas (R.A) the Messenger (Peace and Blessings of Allaah be upon him) said, "If anyone of you, when having sexual intercourse with his wife, says (This Du'a) and if it is destined that they should have a child, then Satan will never be able to harm him."

[Bukhari - Volume 7, Book 62, Number 94]...

Cikin firgici Islam ta nemi ‘kwace kanta, jin yadda Saifullah yake shafa ta

A hankali ya shiga shafa bayanta zuwa gashin ta, cikin rad’a rad’a yace da ita,

“Wane turare ki kai using a gashin ki, it smells nice..”

Cikin rawar jiki da baki tace,

“Strawberry conditioner ne na product din body shop..”

“Love... calm down.”

Cikin tab’o cikin rigar ta ya lura ba komai a jikin sai rigar baccin ta, ahankali yace da ita,

“Love...”

“ummm!!”

“I want you, let’s make this day romantic and most memorable pls..”

Mutuniyar ku da alama tsumin da Fatima ta bata yafara aiki, a hankali Islam tace

“I want you too”

Haba Saifullah sai ya dauki ragaman aiwatar dakomi lokaci guda yafara bata hot kisses a lebanta, ita kuma Islam sai take kokarin suma, bata ankaraba taji Saifullah yayi fatali da rigar ta, ranar Islam taga abin mamaki, Saifullah sai faman sumbatu yake unnecessary, jikin Islam ya

fara rawa, Saifullah ya lura da hakan yace da ita,

“Love! do not be afraid, I'm not gonna hurt you insha Allah! I promised to be an excellent lover”

Islam dake rawar jiki tace,

“ I know you are not gonna hurt me... And I love yo...”

Bata karasaba Saifullah yafara aikamata hot kisses, tuni ya mai da Islam cikakkiyar mace aranar da lallami da komi, yana kuka tana kuka, shi kukan dad’i ita kukan jiga ta, Duk koda shi dinma ya jigata kwarai matuka.

Ni miss xoxo naja masu kofa dan nafara wuce hurumina, sannan naxauna abakin kofa inajira! Yau dau burin masoyan ya cika ko kuma nace burin ango Saifullah yacika aure yau kusan wata 3 amma sai yau hakarsa tacimma ruwa, kafin gari yawaye Islam ta gane kuranta, Don kusan kwana sukai ana abu daya saida yaji kiran sallan farko kafin ya kyaleta, sai da suka shiga bayi don tsaftace jikinsu nan Saifullah yalura ya galabaitar da Islam, sosai yatara ruwan xafi da Dettol yasa tashiga ta gasa jikinta,

Cikin shagwaba yace,

“nima barin shiga ruwan xafin, Dan yau Love tayi dis virgin dina nima”

Ita dai Islam shiru tai, ya shrya yatafi masallacin asubah! ita kuma Islam tayi tata agidah,bayan yadawo daga masallaci yadau waya yakira wajen ppa dinsa yace yau ba zai samu zuwa ba, , abashi absence leave na sati d’aya. Sannan yakalla IsLam datai kasa da idonta tanajin kunya, Saifullah yai daria kafin yace,

“ Kinga kafin nan mun fara renan unborn baby dinmu ko?!”

itade Islam shiru tai.,Saifullah ya lura kunyar sa take ji yanzu, tun da su kai auratayya, a hankali yace.

“Toh tunda ba zaki magana ba shikenan, amma Ina mika godia ta agare ki, nagode sosai gaskia kin cika yar halas da baki zubar da mutuncinki awaje ba, Don kin nuna lallai iyayenki sunyi maki kyakkyawar tarbiyya, Thank you so much fa, Don wallahi na samu Mrs Saifullah din dai-dai, Ni na bude kayana, kuma nima kin same ni sabo, gaskia I’m truly grateful zuma na, duk da na sha rakin kiran su Ammi and plenty of others, Thank you so much, Allah ya bamu zuri’a dhayyiba Ameen..”

“Ameen”

Islam ta fad’a, hade da runtse idanu saboda zafi da zugin da ‘kasan ta keyi,

Safiya nayi Saifullah yafita siyo masu abinci a eatery, Islam ita kadai akan kujera sai murmushi take tayi, tayi wankan ta cikin kananan kaya, wando 3quater, sai rigar yar karama da ita, Sosai tayi kyau abinta, Sai kamshi take. cikin xuciarta tace,

“Saifullah kenan, mai kima da hak’uri, ya Allah kabar ni da Saifullah dina, namiji daya tamkar da dubu”

Sai tayi murmushi takuma ce

“Lallai soyayya lokacin da xata shigi mutum bata shawara..”

Ko da Saifullah yadawo shima shigar tasa kaman ta matarsa short nickers yasa da riga yayi kyau abinsa, brown eyes dinsa sai shining suke, Yazo gabanta yadauketa yadora ta kan lap dinsa ahaka yai feeding dinta abincin daya siyo musu, ita dae sai kunyar shi takeji, yai murmushi,

“Wai Love meyasa kikejin kunyata yanxu bayan mun riga da munxama daya, babu kunya atsakaninmu”

Ya kafe kan lallai sai ta kalli cikin idonsa, Islam ta kasa, da cakulkuli da komai yasa Islam takalla cikin idonsa sai Saifullah yakashe mata Ido ,gaba daya takasa dauke idonta anasa,Dan wani kyau da kwarjini ta ga yamata, Idonshi yatafi da ita ga kuma wata so da shakuwa data gani ta karanto cikin idonsa...kawai tasa hannu tafara taba curly hair dinsa dasu kai yala yala kaman gashin jarirai da idonsa da lips dinsa, Nan suka shiga tab’e tabe junan su, romancing kawai nothing beside the romance.

Ko da dare yayi, Arabian shi ga su kai, suka nufi wani wajen cin abinci bayan sun dawo suna xaune a parlor, suna shan milkshake, kan Islam akan cinyar Saifullah tace,

“‘Dan kira mun waya ta, bangan ta ba..”

Daga kai Saifullah yayi, ya kira wayar tata, ashe suna zaune akan ta ma, Saifullah ya ‘dago wayar yana kallon screen din, ‘suffocating being’ shi ne sunan da yagani a rubuce, Ai kuwa ya cuno baki gaba kafin yace,

“Love ni ne suffocating being, why?”

Ta gimtse dariar ta, kafin tace,

“Ka nason fadan so suffocating shi yasa..”

“Oh ai that was then, lokacin everyday felts so uneasy, and around mutane ina feeling

uncomfortable. Tun ina school word din ya zauna a baki na, and with time it became addictive more like obsession, Thats it kawai, amma ai na rage fad'a, beside zan ma dena fada. Saboda ke, you mean the world to me, I love you more than life it' self..."

Islam tayi murmushi in awwwn mood, kafin ta hade bakin ta, dana shi, sun jima a haka, kafin tace,

"I love you most sugar..."

_A gurguje_

Haka rayuwar su ta kasance, kullum suna cikin bawa soyayya hakkin ta, duk da tsakanin harshe da hak'ori ma ana samun sab'ani,Toh suma sukan dan samu sab'anin, amma dake sun riga da sun fuskan ci juna, ba sa jima wa suke shiryawa abun su, kullum suna cikin soyayya, kamar cin 'kwan makauniya, da haka har Aji Mommodu ya biya musu umrah su dasu Khaled suka je, Bayan sun dawo ne Islam ta fara laulayin ciki, daga k'arshe, Sai deferring semester tayi, ana scanning aka ga yan biyu mace da namiji, Both familyn sunyi farin ciki wanda alqalami ba zai iya rubuta shi ba, cikin ta na tsufa Haj Zuwairah ta dauke Islam, Ai kuwa Saifullah yace bai san xance ba, dole sai da ya bisu ya manne mata, ranar da zata haihu ne kawai baya nan, Ta haifo santala-santalan 'ya'yanta, macen aka sanya mata sunan Haj Zuwairah zasu dinga kiran ta da 'Arya', namijin kuma sunan Alhaji Mommodu suka sanya masa, za'a dinga kiran sa da 'Aryan', Murna wajen Saifullah ba'a magana, domin lokacin sa da soyayyar sa kacokam ya 'dauka ya 'dora akan su,Wani lokacin har kishi take dasu, sai yayi lallami da toshiyar baki kafin ta hakura......

_*DAWOWAR LABARI_*
_*(K'arshen Page 1)_*

Haka bacci 'barawo ya sace Islam, zuciyarta cike take da tuna bayan rayuwar ta, tana ta shek'a baccin ta saifullahi yayo mata reply,

_"Sugar pie.It does not matter how my day was, I always long for the night, to cuddle you all night as you quench my heart.It was a stressful night,aiki muke tayi yanxu ma muna construction site na ikeja... A shafa min kan Arya da Aryan...I love you more than life itself. Goodnight my love.."_

*Da* Asubah ta farka saboda kukan 'yan biyu, Sallah ta fara yi, sannan ta basu Mama suka sha,suna gama sha kuwa suka koma bacci, ita kuma ta tashi ta sauka kasa, lokacin Hinde mai aiki har ta gama shara ta fara mopping, ta yata Islam tai da wasu abubuwan, sai takwas saura ta koma sama, tayi wanka, ta yiwa yan biyun nata wanka, da sauri ta kintsa su, Saboda asibiti zata kai su, akwai monthly shots (allura) da ake musu na kariya daga kamuwa da cututtuka. Sai a sannan ta janyo wayar ta, message din Saifullah ta karanta tana murmushi, reply ta masa kafin ta kira shi su gaysa, inda yake ce mata sai jibi zai dawo, kamar za tai kuka ta yi masa

fatan alkhairi da Allah ya dawo dasu lapia...

Hinde na rike da Arya ita na rike da Aryan suka shiga mota, driver ya jasu, dake tunda tasamu ciki, Saifullah ya hanata driving gaba d'aya, sai driver ne ke kai ta duk inda zata, suna zuwa asibiti suka nufi wajen likita, yayi duk abunda zai musu, sannan suka je farmers market inda tayi y'ar siyayyar cefanan ta, sun jima kafin su dawo gidah, suna dawowa gidah tun daga parking space taji gabanta na fad'uwa haka dai ta danne, suka karasa cikin gidan, Ta haye sama da yaranta, Hinde kuma tai kitchen tana jere kayan da suka siyo a ma'adanan su.

Kamar daga sama ta jiyo muryar Saifullah, a razane ta juya tana duban sa, kashe mata ido d'aya yayi kafin yace,

"Surprise.."

Hawaye ne suka shiga reto a idanun ta, karasawa tai ta rungume shi tana dukan kirjin sa, murmushi yayi yana kara manneta a jikin sa, sun jima a haka kafin ta goge hawayen ta tace dashi,

"Me zaka ci? Na dafa maka yanzu Zawj"

"Love! A koshe nake wallahi, ni yanzu abunda nake so kawai ki kaiwa Hinde yan biyu, nayi missing dnki wallahi, a matse nake.."

Daria tayi, kafin ta sauka 'kasa da yan biyun ta, ta bawa Hinde su, Sannan ta koma sama. Tun a parlor suka fara, zuba lobayya, daga baya ya dauketa cak sukai daki, anan suka gwangwaje suka rakashe yadda suke so, kafin su tashi suyi wankan tsarki, sukai sallar la'asar da aka kira, Saifullah ya dubeta yana murmushi kafin yace,

"Hakika kece rayuwa ta Love, you are my fantasy my only desire, ina son ki, So mai tsanani, Nagode wa Allah da su First Love, da suka hada aure na dake, hakika ZAB'IN IYAYE, Yafi SON RAI, ban taba soyayya ba sai a kanki, kuma akanki na fara sanin 'ya mace, kin shayar dani zumar da ban tab'a 'dan'dana ba, Allah ya bar min ke har abadan da'iman, kuma ina rokon Allah yasa zaman mu ya dore har aljannatul frdaus. Ameen!"

Peck Islam ta bashi kafin tace,

"Nima ina son ka Zawj, ba zan taba dena iya son ka ba *KAI MIN HALACCI* (littafi na da zai zo muku a ZAFAFA BIYAR on 7 dinnan Insha Allah) a rayuwa, ka na 'kauna ta fiye da tunani na, Allah yasa mutu ka raba ni da kai, bazan tab'a bijere maka ba Zawj, Insha Allah har a aljanna frdaus kai ne miji na.."

"Insha Allah love, Allah ya raya mana babies din mu, cikin lapia da kwanciyar hankali, Allah ya musu albarka su da 'kannen su masu zuwa, a kai-kai.."

"Ameen"

Cewar Islam tana daria, bakin ta ya tsosa kafin ya sake cewa,

"We are meant to be fa, ko sunan mu ba ki ga ya bada ma'ana ba?*SAIFUL_ISLAM...💕* Kinga yana nufin 'Takobin Musulunci'..."

Da haka ya rufe bakunan su da wani irin sweet and passionate kiss mai bin magudanar jini da tsoka....

_And they lived happily ever after_
_The End_

_TAMMAT BI HAMDULILLAH_*

_Love is patient love is kind it does not envy it does not boast its not proud it does not dishonor others,it is not self seeking,it is not easily angered it keeps no record of wrongs,Love does not delight in evil but rejoice with the truth,it always protects,always trusts,always hopes,always perseveres#SAIFUL_ISLAM2020_

_Toh komai yai farko zai yi k'arshe, duka-duka anan ni Nana Hafsatu nakawo k'arashen littafina me suna a sama😊kun san shi d'an Adam ajizi ne tara yake be cika goma ba, duk wanda nabatawa rai farawar littafinnan zuwa k'arshensa ina neman yafiyarsa,ina fatan dan fadakarwar dake ciki Allah yasa mu amfana da ita,kurakuren ciki rabbi yayafemun.._

_First of all I wanted to thank each and everyone of you reading this,thank you for reading my story,thanks for the calls,messages and comments I wholeheartedly appreciate it..kusani har kullum kuna ran Nana Hafsaatu,da baxakar ku nake rawa my fans..Fatana Allah yabar mu tare.MISS XOXO na yinku beyond words😊Rabbi yabar zumunci.._

_Wannan littafi kacokan naki ne, sadaukarwa ne agareki my cutest boy, *ASY KHALEEL*,Rabbi yabar mu tare har abadan da'iman, Allah ya baki miji na gari tawan, Ina miki son so fisabilillahi, May you be forever blessed😍❤️Alhamdulillah! Na sauke alqawarin da na miki shekara da shekaru._

_To my *YA HAJJA CE* the best of them all, my hero, my biggest supporter, Wannan littafi TUKWICI NE agareki I just want to thank you from my cheesy romantic heart for supporting SAIFUL_ISLAM, for recommending it to others, most importantly for believing in me😊and supporting me to finish this story,,Thank you so much kedin tadabance a xuciyata,Allah yaraya mana ihsan da Areef. Yabarku tareda Uncle har abada😊👌🏾 _

_Tawan tawan, 💋💕My BILLYN ABDUL mi fren, mi love, mi best❤Wannan littafi TUKWICI ne

kema agareki😊a har kullum alkalami na baxe iya rubuta dimbin godia ta agare ki ba kalmomi sunyi kadan wurin kwararo kalaman matsayin ki awajena,Rabbi yabar mu tare matar Uncle abdul,Allah ya Kara dankon soyayya tsakaninki da Uncle Abdul, Allah ya azurta ku da abunda kuke nema dunia da lahira😊Ina sonki Kina raina akoda yaushe.._

_INA YAN WORDPRESS?!THANK YOU SO MUCH FOR THE COMMENTS LOVE AND CARE❤I LOVE YOU GUYS BEYOND YOUR WILDEST EXPECTATIONS🧡🧡_

_INA MASOYAN SAIFUL_ISLAM? TO KU MATSO KUSA, DOMIN LITTAFIN *KAI MIN HALACCI* DA ZAI ZO MUKU A 7 GA WATAN JANAIRU 2020, INSHA ALLAH💋LITTAFI NE DAKE CIKE DA DARUSSA KALA KALA, BANGAREN SOYAYYA KUMA BA'A MAGANA DOMIN *SOYAYYAR SHAMSUDDEEN DA ALIYA*, TA ZARCE TA SAIFULLAH DA ISLAM😍💕❤️,GA MAI BUKATAR LITTAFIN *KAI MIN HALACCI DA MA SAURAN LITTAFAN ZAFAFA BIYAR*, ZAKU IYA TUNTUB'AR LAMBOBIN MU...._

*_Daga ƙarshe muna muku albishir da zuwan zafafa biyar insha ALLAHU a ranar 7 ga watan janaury nan da muka shiga, muna fatan waɗanda basu sayaba zasu garzayo kusa suma ayi dasu, dan har yanzu hajarmu abuɗe take a gareku, shima wannan babban halaccine da zaku nuna mana wanda bazamu taɓa mantawa dashiba, zukatanmu sukuma yarda kuɗin masoyane na gaske😄🙏🏻🙈_*.

_ZAFAFA BIYAR MASU ZUWA A 2020 INSHA ALLAH._

*ƊAURIN ƁOYE!* (Safiyya Huguma

*SAUYIN ƘADDARA!* (Hafsat rano)

*KAI MIN HALACCI!* (miss xoxo)

*BURI ƊAYA!* (Mamu gee)

*WUTSIYAR RAƘUMI..!* (Bilyn Abdull)

👇🏻karku bari ayi babuku

*ga mai buqatar littafan zafafa biyar dukansu ko wasu daga ciki sai ya biya 500 ga dukka litattafan,ko 200 ga littafi  daya,ko 300 ga littafi biyu,ko 350 ga liitafi uku,ko 450 ga littafi hudu*

*za'a tura kudin ta wannan accnt number din*

Hafsat kabir umar

0225878823

GT bank

Saika tura shaidar biya ga wannan number

08030811300

Ga masu turo da katin waya kuma zaku tura katin MTN  ta wannan number din

07067124863

Da zarar kin biya kai tsaye zaki tsinci kanki cikin gidan da zaki samu littafin da kika biya.

*Karki bari ayi babu ke*🤝🏽🤝🏽🤝🏽

_NI CE DAI TAKU;_

_*NANA HAFSAAT MOMMODU HADEE
__*(MISS XOXO🧕🏼)_*

_*WRITTEN BY THE ELOQUENT WRITER;MISS XOXO🧕🏼_*
[1/3, 10:56 PM] Miss Xoxo: SAIFUL_ISLAM💕

BY MISS XOXO

Mai mata posting kullum bilyn Abdull🤐 🤓 😣.
Karta dakani wasa nake🏃🤣